[7/26, 11:32 PM] Jiddah Aliyu: *GIDAN RINA*

An dauko wannan littafi daga shafin www.dlhausanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.dlhausanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2348140419490

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.dlhausanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2348140419490 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC

those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT

__

Na

Hauwa Shehu Aliyu
{Jeeddah Aliyu}

*Bismillahim rahamanin rahim*

*HASKE WRITERS ASSOCIATION*

_Godiya ta tabbata ga Allah madaukaki sarki ina gode masa da ya bani ikon rubuta wannan littafi._
_Kuma ina neman gafararsa, haka kuma ina neman taimakonsa, ina neman tsarin Allah daga sharri mutum da Aljan, Allah yak'arawa Annabi Muhammad{S.A.W} daraja yasa muna ciki wanda zai ceta ranar alk'iyama Amin._

_Gargadi:- Ban yarda wani ko wata ya juya min labari ta kowace siga batare da izzini na ba Saboda haka akiyaye._

*FREE PAGE*

*1*

*Abuja*
*Maitama*
*10:47am*

Hajiya Zaituna tana zaune akan d'aya daga cikin lutsuma-lutsuma Royal chairs da suka k'awata tankamemen sitting room d'inta, mai kama da na president saboda girma da k'awatuwarshi.
"Kyakyawa macce mai cikar halitta fara sol da ita kallo d'aya za kayi mata ka gano buzuwa ce, shekaru ta na haihuwa ba zasu zarce hamsi da biyu zuwa da uku ba.
Jikinta sanye da shadda kamfala orange in colour irin na k'asar Mali, sai kyali da daukar ido take, wuyanta da tsintsiyar hannunta had'e da yatsunta sun sha ado na gold k'irar Dubai.
"Duk da kasancewar shekaruta sun tafi, hakan bai hanata fente fuskarta da makeup ba.
"Duk da wannan uban ado da ta ca6a bai hanawa fuskarta baiyanar tsan-tsan damuwar da take ciki ba.
jin take kamar ta daura hannu aka ta kurma ihu azahirin gaskiya yau ta kasance mata ranar

mafi muni arayuwarta, rana ce da zata ruguje mata burinta na tsawon shekaru masu yawa gaske.

Ba ko shakka wannan ita ce the most terrible day arayuwarta.

Wani kafirin gwaron numfashi ta sauke, kamar ta yi gudu ceton rai, babban tashin hankalinta bai wuce aure da mijinta Alhaji Muhammad Ardo yakeso d'ata Aliyu ya yi, duk duniya ba abinda ta tsana irin Aliyu ya yi aure abinda bata fatan faruwarsa.

"Duk tasan d'an nata yafi ta tsanar aure ko kalmarsa bayaso a anbata masa, shiyasa duk lokaci da ta tuna da hakan sai taji hankalinta ya kwanta.

"Sautin muryar mijinta ta ji yana kiran sunanta zuciyarta ta buga very fast babu sharri ta mik'e tsaye har tana had'awa da dafe k'irji.

"Alhaji har kafito....?

Tafad'a cikin rawar murya.

Eh.....nafito kinsan jirgin 12 noon za mu bi, kuma sai mu biya ta gidan Alhaji Yusuf saboda tare, za mu tafi Suraj kuma nayi waya da shi ya ce mu had'u Airport.

"Ina Sultan ko har yanzu bai gadi fitowa ba?

so yake sai ya6ata mana lokaci.

Ajiyar zuciya ta sauke cike da fargaba ta ce Alhaji akwai matsala fa.

"matsala kuma?

Yafad'a yana mata kallon mamaki?"

"Eh...Al...ha..ji..Sultan baya gidanan nima da asuba naga text dinshi ya wuce Scotland.

Ashe ya yi booking jirgin da asuba suka d'aga....

Ke! Ya isa!

Alhaji yadaka mata tsawa azarane ta ja da baya.

Cike da zallan masifa yafara fad'a ni Sultan yakeso ya kunyata, ni yakeso ya mayar k'aramin mutum to wallahi bai isa ba.

"Wannan shine karo na hudu ina nema masa aure yana ruguza shi, da izzini ubangiji a wannan karo aure nan ba zai lalace ba ko don albarkacin addu'a da ake min akansa.

Na rasa meke damu shi da ya tsani raya sunnah ma'aki{s.a.w}

"Amma ba laifinsa bane duk abinda yake yi agidanan ke ki ke daure masa gindi, daga ke har shi a sannu zan yi maganinku, tafiya Yola nema masa aure babu fashi, ba Scotland yatafi ba in iya yatafi birnin sin duk uwarsu d'aya ubansu d'aya awurina.

"Na tabbata ba wani scotland da yatafi ina barin garinan zai dawo cikin gidanan, ki fad'a masa ya gama karyayyakinsa gaba d'aya za mu had'u sai naci ubanshi ba dai ni ya wulak'anta ba.

Cikin kwantarda murya irin na mace mai biyayya ga miji Hajiya Zaituna ta ce

"Ka yi hak'uri Alhaji ka bi komai ahankali, ni sai nake gani kamar akwai matsalar da ta ke hana shi aure...

Ke bak'ar al-mura rufe min baki, har ni za ki kawowa chanfe-chanfenku na mata mtswww..!

Yak'arasa magana had'e da jan dogon tsaki, gani za ta 6ata masa lokaci yasa bai k'ara tamka mata ba yanufi k'ofar fita yana mai cigaba da 6am6ami fad'a kamar ya ari baki kare.

"Tana gani yafita ta dauki wayarta tai dialling digit d'in Sultan ta kara akunnenta
Hello....yarona nasan kana cikin garinan na rok'e ka, ka dawo gida inaso magana da kai.
Tak'arasa magana kamar za ta yi kuka.

"zamanta ke da wuya girls d'inta su uku suka shigo kowace da shigar English dress, su yi matukar kyau da ka kalle su kasan ita ta haife su.
Tima ce tafara magana cikin sanyi murya ta hanyar cewa, momma ki ji tsoron Allah ki tuna za ki mutu za ki kuma riske abinda ki ka aikata yana jiranki a kabarinki.
Ya Aliyu d'a ki ne da ki ka haifa da kanki a cikinki momma, I don't know why da bakyaso ya yi aure kullum k'ara masa tsoron mata da tsanarsu ki ke narasa miye ribarki na yin hakan idan ma hud'ubar shed'an ki ke bi za kai ki ne yabaro.
"Har Tima ta dasa aya azanceta momma tana kallonta.

"Girgiza kai momma ta yi ta ce Allah yaye miki wannan ciwo Tima, kina dauke da wannan lalura wa zai aure ki.
Turo baki Tima tayi ta firfito da idanunta, enough momma yakamata zuwa yanzu kidaina danganta ni da ciwon hauka ni lafiyata qalau bani dauke da kowace irin cuta.
Kawai dai ina k'ara tunatarda ke ki dinga tunawa da mutuwa ehee...

"Abinda zai ba ka mamaki saura girls d'in biyu kamar ba su cikin sitting room d'in kowace ta mayarda hankalinta a wayarta tana operating.
"Momma ta juya ta kalle girls d'in ta ce Zee-zee!
Na'am!
Yau Tima ta yi taking medicine d'inta kuwa?"
Ban sani ba momma saboda batare mukayi breakfast ba.

Minat ce d'ago ta dubi momma ta ce tasha.
"Tima ta yi karaf ta ce ban sha ba a sink na zube shi nayi flushing shege.
Cikin taussasa halshe momma ta ce saboda me ba ki sha ba Tima?"
Kin kuma san irin illah da rashin shan magani yake haifar miki.
"Mtcwww.....!
Tima ta ja tsaki had'e da wulga mata harara,
ai na fad'a miki ba zan k'ara sha ba.
"Tausayinki nake ji momma saboda akwai ranar k'in dillanci ranarda zani maigari ya6ata, muddin momma ba ki tuba ba ki ka komawa Allah idan kin mutu sai an jefa ki wuta jahanama, ga ki ga fir'auna.
"Ya sallam.....Tima ni ki ke had'awa da fir'auna?
Momma tafad'a tana zaro idanu, amma ba yin kanki bane shed'anu aljannu da suke tare da ke ne.

"Murgud'a baki Tima ta yi tana harara momma ta ce ba wani aljani da na ke tare shi.
Momma tafashe da kuka tana cewa Ya Allah ka ba wa yarinyar nan lafiya, in ban da sharri Jinni yarinya ba wacce ta ke zagi sai mahaifiyarta.

Minat ta mik'e tsaye ta rik'o hannun Tima ta ce zo mu tafi little sis ki sha maganinki kinga a dalili misbehaved d'in da ki ke kinsan momma kuka.

"Zee-zee ta ce gara ki ja ta ku tafi yanzunan sai su 6atawa mutum mood.

"Minat ta yatsine fuska had'e da kya6e baki ta ce mu je kinji k'anwata.
Janyo ta ta yi suka nufi bedroom.
Adai-dai lokaci Aliyu, ya shigo sanye da farar shadda, fuskarshi a muturk'e.

kallo d'aya Zee-ze tai mishi ta dauke fuska, da kyar ta bud'e baki ta gaida shi saboda tasan halinsa ba lalle bane ya amsa gaisuwarta ta ba, ya amsa ko bai amsa ba ita kan mik'ewa ta yi ta bi bayan 'yan uwanta.
Momma nagani shi tafara rawar jiki.

"Zo nan yarona!

Tafad'a tana mik'a masa hannunta.

"Ya kalle hannun nata ya dauke fuska yanufi two sitter ya zauna yana yatsina fuska, kamar ance mishi ya zauna dole.

"Momma ta gyara zama tana fuskantarshi Yarona Daddynka fa yace wannan karon sai yai maka aure, baya bukatar amincewarka.
Tak'arasa magana tana kallo yanayinsa.
"Tsawon lokaci yad'auka yana jujjuya zoben yatsanshi, kamar ba zai yi magana ba saida ya tsotsi lower lip d'inshi cikin sanyi murya ya ce ni fa banaso aure kwata-kwata arayuwata, banta6a kallo wata 'ya mace naji ina sha'awarta ko sonta asalima tsoronsu nake.
"Please momma ki ganarda Daddy ya hak'ura da zance aure nan, ko yanayin business d'ina kadai ba zai barni na ba wa matata kulawa ba.
"Duk wani business na Daddy ni kadai nake handle d'inshi, Sauki d'aya uncle Suraj yana taimaka min ni kaina bana da hutu yaushe nakeda lokaci wata 'ya mace.
yak'arasa magana yana squeezing face d'inshi.
"Momma tasaki 6oyayye murmushi dad'i ta ce ba abinda ban fad'a masa ba, ya kafe akan lalle sai ya yi maka aure narasa dalilinshi naso yi maka auren dole.
Awannan zamani ko mata andaina yi musu aure dole saboda kai yawaye, balle irinka Sultan ace za'ai maka dole.

"Tak'arasa magana tana girgiza kai.
shiru Aliyu ya yi had'e da lumsashe manya idanunshi.
"Momma ta cigaba da cewa shi aure lokaci ne da shi.
Ni aganina lokaci aurenka ne bai yi ba.
mahaifinka yak'i fahimta cewa kai ba mata ka ke nema ba awaje ka tsare kanka narasa hujja

Alhaji na nacewa akan lalle sai ya yi maka aure.
"Tsorana d'aya yarona bansan wacece yarinya da za'a aura ma ba.
Matan zamani nan ba kowace ke da imani ba, yadda mahaifinka yake da tarin dukiya kuma kai kadai ne d'asa namiji, duk wacce ta aure ka ba don Allah za ta aure ka ba burinta mahaifinka ya mutu ka gadi dukiyarsa, ita kuma ta kashe ka ta mallake dukiyar ita kadai karka yi mamaki hatta ni da 'yan uwanka sai ta kashe.
"jin abinda tafad'a yasa Aliyu sauri bud'e idanunshi, yana kallonta gani yadda yake kallonta yasa tafara kukan makirci, ta na cewa Allah kadai yasan abinda zai faru anan gaba.

"Momma please stop cry banaso kina imagination d'in mummuna abu akaina, in fact ba ni kadai bane d'an masu arzki duk saura mata basu kashe su ba sai ni.....kisaki ranki momma ba abinda zai sameni.
"Ba za gane ba Ali duk lokaci da na kwanta barcci sai nayi mummuna mafalki akanka.
"Whatever!
Yafad'a yana ta6e baki shi fa har ga Allah yafara gajiya da tsoki burutsu momma, saboda ya kawo karshe zance nata ya ce Momma ba kowane mafalki ne yake zama gaskiya ba.
"Waya gayamaka?"
momma tafad'a tana zare idanu gata da manya idanu tubarakallah masha Allah!"
"Har ta karkace baki za ta cigaba da zuba yakatsi mata hanzari ta hanyar cewa please momma I have some works to do.
Murmushi dole ta yi had'e da cewa tashi katafi but you better think what am saying clearly.
"Yes momma!"
Yafad'a yana mik'ewa da sauri yanufi apartment d'inshi tun kafi tasake tsayarda shi da wani zance.
*******----*****
*Adamawa-Yola*
*1:34pm*

Ahankali take tafiya yayin da take fitowa daga chief magistrate court 1 hannunta na dama rik'e da black coat dinta yayin da, d'ayan hannunta rik'e da handbag duk da ta yi winning case d'in da take wakilta amma fuskarta babu walwala.
"Sai tafiya take tana rangaji kamar marar lafiya, yanayinta kamar wacce batada lakka a jiki.
Barrister Barkido!"
Ta ji ankwala mata kira ta bayanta.
Jin murya wacce ta kira ta yasa ta tsaya chak, batare da ta juya ba.
K'arasowa Barrister Zarah ta yi fuskarta cike da mamaki ta ce...what wrong with you?
How could you leave the court bayan kinsan will should talk barrister Jamil about the original document da ke hannunshi.
"OMG!"
Tafad'a tana dafe goshi tsawon sixteen seconds ta dauka dafe da goshi, kafin ta ce please Barrister Ladan I really wants to go home, za ki iya kar6a awurinshi sai ki ba wa clients d'in.
"Shikenan bari naje amma ki jirani a mota za mu yi magana.
"Okay.....

Tafad'a had'e da cigaba da tafiya wurin da ta yi parking motarta ta  kirar Range rover elegance 2019 tun kafin ta k'arasa ta yi unlock d'in motar da remote da ke had'e da carkey.
Back sit ta bud'e ta jefa coat d'in.

"Amaimako ta shiga motar sai kawai ta jingina jikinta ga motar, ta yi holding hands d'inta a k'irji tana kallo mutane da ke kai da kawowa a harabar kotun.
"Ba'a dauki dogon lokaci ba ta hango Barrister Zarah Ladan.
Har tak'araso bata dauke idanunta daga kanta ba.

*ALK'ALUMA SHIDDA GARABASA 2020*

_SHIN WAI MA TA INA YADACE IN FARA NE? *TANA K'ASA TANA DABO* GASHI INA GANIN KAMAR *DA CIWO A ZUCIYA TA* HAKAN NE MA YASA NAKE JAJURCEWA A KODA YAUSHE WURIN NUNA *IZZATA* DOMIN CIKA *BURIN ZUCIYA TA* DUK DA INA TSORON TAB'O *GIDAN RINA* DOMIN YIN HAKAN TAMKAR YIN SARSTSE NE GA *RAYUWATA* HMMMM AI HAKAN NE MA YASA NI *UMMI A'ISHA* NAKE KIRA GARE KU MASOYA NA MA'ABOTA KARANTA LITTATTAFAI NA DAMA LITTATTAFAN K'UNGIYAR HASKE WRITER'S ASSOCIATION GABA D'AYA DA KUZO MU YI DANDAZON, CINCIRINDON KARANTA *DA DUMI DUMINSU LITTATTAFAI GUDA SHIDDA* WAD'ANDA SUKA SAMU KULAWA DA TAGOMASHI DAGA MARUBUTA SHIDDA FASIHAI KUMA HAZIKAI WATO *YAN SHIDDA AMANA*

_SUNE KAMAR HAKA_
AISHA DAN SABO👉🏻 *BURIN ZUCIYA!!*
SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR NAN MAI *LAIFIN BOYE DA HURAYYA*

JIDDAH ALIYU👉🏻 *GIDAN RINA!!*
DAGA SHAHARARRIYAR MURUBUCIYAR *NI DA YAYA HABEEB DA SONKI NE SANADI*

KHADIJA AHMAD KDEEY👉🏻 *DA CIWO A ZUCIYATA!!*

DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR NAN MAI *ABU IRFAN DA Y'AR BABBAN GIDA*

RAHMA NA LELE👉🏻
*RAYUWATA!!*

DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR NAN MAI *LIKITAN ZUCIYA DA SAMARIN BANA*

SLIMZY👉🏻 *IZZA TA*

DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR *ANYI WALKIYA DA TAK'ADDAMA* WANDA YANZU HAKA YAKE ZUWA MU KU A KYAUTA

SAFIYYA GALADANCI👉🏻 *TANA K'ASA TANA DABO!!*

DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR *RUBUTATCIYAR KADDARA*  WANDA YANZU HAKA YAKE ZUWA MU KU A KYAUTA.

KAR KUBARI ABAKU LABARI NI DAI TUNI NA HADA KOMAITSA NA NAYI GABA DOMIN KUM SAN BIKIN FARAR KAZA BALBELA BA SAI ANBATA GORON GAYYATA BA, KAR DAI KU MANTA WADANAN MARUBUTAN DAGA KUNGIYAR NAN MAI ALBARKA KUMA HASAKKAKU WATO *HASKE WRITER'S ASSOCIATION*
*ALK'ALUMA SHIDDA AMANA*

_GA MAI BUK'ATAR KARANTA WADANNAN K'AYATATTUN LABARAI ANYI MASU KUDI NE AKAN NAIRA DARI BIYAR 500 KACAL GUDA SHIDDA, MAI SON GUDA D'AYA ZAI BIYA 200 MAI SON BIYU 350 MAI SON HUDU ZAI BIYA 400_

*SAI KU TUNTUBE MU KAMAR HAKA*

FIRST BANK
3120641551
SAFIYA MUSA GALADANCI
SHAIDAR TURA KUDINKA GA WANNAN NUMBER
08103943903

👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
ZENITH BANK
2255398727
AMINA JIBRIL
SHAIDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER
08166177830

GA MASU TURA KATIN WAYA MTN AKE BUKATA ZAKA TURA GA WANNAN NUMBER 08039424298 SHAIDAR BIYAN KATINKA GA 07084161619

KADA KUBARI A BAKU LABARI!!!

DOMIN K'ARIN BAYANI
👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
07084161619
08103943903
08166177830

Jeeddah Aliyu

[7/26, 11:34 PM] Jiddah Aliyu: *GIDAN RINA*

Na Jeeddah Aliyu

*FREE PAGE*

*2*

Isowar Barrister Zarah Ladan  ya yi dai-dai da tana lumshe idanunta, daga bisani ta bud'e su key ta mik'a mata batare da ta yi magana ba.
"Barrister Zarah ta kar6i key d'in saboda ta fahimce me k'awartata take nufi.
sit d'in direba ta zauna yayin da Barrister Barkido ta zauna gefenta, har lokaci da damuwa akan fuskarta.
Saida Barrister Ladan ta kalleta na wasu 'yan dak'ik'u ta gargiza kai, sannan ta ja mota.
"Bayan sun hau titi barrister ladan ta dubi barrister Barkido sosai sannan ta yi concentrated tuk'i da take.
"Meke damunki bebs naga tsananin damuwa akan fuskarki?"
Barrister Barkido ta d'an ja tsaki tare da sauke ajiyar zuciya, ta ce ki bari kawai bebs yau kwata-kwata bana cikin natsuwa Allah ne kawai yanufi za mu yi winning case d'inan.
"Uhm! Gaskiya ne amma meke damunki ne?"
"Ta d'an gyara zamanta ta fuskanci Barrister Ladan sosai, ta ce abubuwa da yawa, za ki yarda ida nace da ke daren jiya ban runtse ba, yadda naga rana haka naga dare.
sai juyi nake yi akan bed har asuba.
"Gaba d'aya Barkid'o ya d'aga min hankali, har na rasa inda zan sa kaina.
"D'an waigowa Barrister Ladan ta yi ta zubawa Barrister Barkido ido gani yadda damuwa tak'ara bayyana k'arara, akan fuskarta ita ma sai ta ji ba dad'i saboda amintaka da shak'uwar da ke tsakaninsu tasamo asali tun suna yara.
"Ta nisa tare da girgiza kanta ta ce ko ba ki fad'a ba nasani bebs, saboda the whole week d'inan ba ki cikin hayyacinki, nishad'i da walwala sun k'aranta agareki  na zuba miki ido ne nagama karantarki.

"Now tell me what's exactly wrong with you....?
Sassanyar ajiyar zuciya Barrister Barkido ta sauke, sannan ta d'an yatsina fuska wanda d'aya daga cikin d'abi'unta ne  wanda wasu mutane masu karancin fahimta suke mata kallon tana da wulaqancin.
"Ta ce wallahi bebs komai ya dagule min, ki taimakeni da shawara.
"Inajinki!
Cewar Barrister Ladan.
"Shin ko kinsan yau za'a zo neman aurena daga Abuja?"

whats!

Are you serious?

Sake yatsine fuska ta yi fiyye da farko, tare da d'aga girar idonta.
"Bebs ba ki da kirki shine sai yanzu ki ke fad'amin.
"I knew bebs za ki ce haka da farko ban dauki abin da mahimmanci ba sai gashi abin is getting serious but am sorry.
"Shikenan bebs na hak'ura amma yaushe ki ka yi boyfriend da ban sani ba?"
"Uhm! Da zan yi boyfriend you're the first person da za ki fara sani.
"Bebs am confused kin k'ara jefa ni a duhu, taimaka fito da ni haske.
"Murmushi Barrister Barkido ta yi wanda yak'arawa kyakyawar fuskarta ma'abociyyar kwarjini kyau, ta ce Barkido ne ya yi min miji.

"What's?
Barkido kuma oh my god!
That's old man ba zai bar mutane su huta ba.
"Mak'e kafad'a Barrister Barkido ta yi alamar ni ma shi nagani.
Abin takaici bansan waye mijin ba kuma aure ba zai wuce 2 months ba.
"Cabdijam!
Lalle this time Barkido ya zo mana da Babban al'amari, amma Bebs miye mafita?"

"I don't know bebs ki nemo mafita before Zuciyata ta buga, kinsan kuma idan zuciya ta buga bebs mutuwa ake yi.
Tak'arasa magana cikin kalar tausayi.
"Dariya Barrister Ladan ta yi ta ce kwantarda hankalinki k'awata kamar kin yi bako ya mutu.
"Mtcwww!
ta ja d'an siriri tsaki
Da ace bako zai mutu da sai na fi kowa murna da farin ciki, kinga abin ya zo min da sauki.
"Wane bako Ki kewa fatan mutuwa?"
Wanda zai zo neman aurena mana.
Sosai Barrister Ladan ta ke dariya saida ta yi mai isarta kafin ta ce, Bebs please mu koma zance mu na farko karki fasamin ciki da dariya.
"Shiru suka yi na d'an lokaci kafin Barrister Ladan ta ce ba za mu yi sauri yanke hukunci ba, k'awata har sai mun had'u da shi idan ya yi miki falillahi hamdu.
"Idan kuma bai yi min ba?"
Barrister Barkido tafad'a tana mai kafeta da ido.
Alokaci za mu nemo mafita sai mu koreshi cikin sauki, kamar yadda mu ka yi wa na baya.
"Ba za ki gane ba Zarah a wannan karon har rantsuwa Barkido ya yi akan lalle sai na kar6i mutume amatsayin mijina.
Kinga kenan zance mu koreshi ma bai taso ba.
"Inna lillahi wa'ina illahim raji'un....ban zace abin ya kai haka ba, yanzu dai mafita guda d'aya ta rage mana dole ne mu duk'ufa addu'a da sadaka Allah ya yi mana kyakkyawan za6i, domin shi kadai yasan abinda yafi dacewa da bawansa.
"Haka ne Bebs amma mazanan suna bani tsoro ko zance aure banaso anayi min, sai gashi

kwantsa lokaci da ban yi zato ba ya riskeni.
"Ki daina jin tsoro minal saboda ba duka gaba d'aya maza suka taru suka lalace ba har gobe akwai nagari akwai bata gari.

"Uhm! Bari kawai Zarah ko iyayyenmu kina kallo yadda suke gwagwarmaya da halin d'iya maza, balle mu da mu ke tasowa wallahi da iyayyena za su kyalleni da zan iya rik'e kaina batare da aure ba.
"Allah ya kiyayye bebs ba ma fata ki k'are rayuwarki batare da kin aurarda jikokinki ba. Barrister Barkido batasan lokaci da dariya ta subuce mata ba, ta ce kai Zarah ba ma 'ya'yana ba.
Eh! mana.
Ita ma tafad'a tana tayata dariya.
Nan take Barrister Barkido ta ji hankalinta ya kwanta damuwar da ta ke ciki ta ragu, shiyasa batada k'awa da ta wuce Zarah saboda duk lokaci da shiga matsala ita kadai take tunk'ara.
"Haka suka cigaba da tattauna zance har Barrister Zarah ta iso k'ofar gidanta, nan suka yi sallama Barrister Barkido ta ja motarta ta nufi gida zuciyarta wasai babu saura damuwa.
****----*****-----***
*WAIWAYE ADON TAFIYA*

*WANENE ALIYU?*
Aliyu Muhammad Ardo shine cikkakke sunanshi, fari ne tass!
Mai matsakanci tsawo yana dogon hancinshi, akan zagayayyar fuskarshi ma'a6ociyya kwarjini.
"Aliyu miskili ne na bugawa a Jarida daily trust shiru-shiru yake bayaso yi doguwar magana yana da zafin zuciya matuka ga sauri fushi da kamar kububuwa.
Aliyu sunan Kakanshi na waje uba yaci shiyasa ake kiranshi da sultan.
"Mahaifinshi Alhaji Muhammad Ardo haifaffen gari Yola ne ya yi ilmin addini da na boko, saidai boko ya fi k'arfi sosai shiyasa ya dusashe na addini.
"Alhaji Muhammad Ardo mahaifinshi Aliyu Ardo a wanchan lokaci mai arziki ne, sosai, ya yi suna har a kudanci Nejiriya k'arin abin ga kuma sarautar da yake da.
"Yana da matan aure har guda hudu da sad'aka guda uku, shiyasa yake da tarin 'ya'ya har talatin da biyu.
Muhammad Ardo mahaifiyarshi Fatima ita ce mata ta biyu, tana da 'ya'ya bakwai ahalin yanzu uku su mutu saura hudu sai d'an kishiyarta Suraj wanda take riko, mahaifiyar Suraj ta rasu tun daga haihuwarshi alokaci Fatima tana goyon Muhammad sai ta kar6i suraj ta cigaba da shayarda shi, idan ba fad'a maka aka yi ba ba za ka ta6a sani ba ita ta haife shi ba.
Muhammad shine d'anta na uku.
"Alhaji Aliyu ya mutu kusan shekaru ashirin da biyar kenan da rasuwarsa.
Matanshi da sadakunshi, da wasu daga cikin 'ya'yanshi sun rasu.
Mahaifiyyar Muhammad tana d'aya daga cikin matan Ardo da suka rasu.
"Duk da haka da yake akwai tarin jikoki shiyasa har yanzu Family din yake da yawa.
Alhaji Muhammad Ardo ya yi karatu boko sosai wanda har ya kaishi da zama Ambassador a England a lokaci matarshi d'aya Maryam tsawon shakaru goma sha biyar da aurensu, Allah bai bata haihuwa ba.

"Da suka dawo Najeriya ya shiga business har ya yi nassarar bud'e kamfanuni da dama arewaci da kudanci Najeriya.
Yana d'aya daga cikin manyan masu kud'in Najeriya.
Yana da gidajen man fetur billa adadin da manya-manya malls a Abuja da Lagos, Alhaji Muhammad Ardo mutum ne mai kafirin neman kudi.
Shiyasa d'ansa tilo Aliyu ya gadesa ba abinda yasani illah neman duniya.
"Lokaci da Alhaji Muhammad Ardo yadawo da England ya had'u da Zaituna Wanda k'aninshi Suraj ya had'a shi da ita.
[7/26, 11:35 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- RUYUWATA

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*FREE PAGE*

*3*

Zaituna cikkakiyar 'yar duniya ce Mai lasisi a hannu, asalinta 'yar k'asar nijar ce iyayyenta sun mutu tun tana da karanci shekaru.

"Hannu k'anwar mahaifinta Adama ta taso ba k'aramar azaba k'anwar mahaifin nata take gana mata ba, Adama muguwa ce ta k'arshe lokaci da Zaituna ta kai shekara goma sha biyar, ta aurarda ita ga wani tsoho mai mata uku ita ce cikon ta hudu.

"Tun daga lokaci rayuwarta tak'ara shiga garari saboda mijin nata Rudda ya fi Adama mugunta nesa ba kusa ba.

Dukan mata yake kamar ba zai barsu da rai ba, yana d'aya daga cikin dalillai da yasa Adama ta bashi aurenta don tasan azaba za ta sha ba kadan ba.

"Ga kuma matsalar kishiyoyinta kasancewar sun fi ta shekaru, sai su dinga had'e mata kai. kullum sai sun kulla mata makircin da Rudda zai daketa saida tadawo tamkar ta6arya kir6a sakwara saboda duka.

"Ana cikin haka tasamu ciki duk da cikin da take dauke da shi, bai fasa lakada mata duka ba. "Cikinta yana da wata bakwai ya daketa kamar yadda yasaba hakan ne yasa ta haifi bakwani, d'a namiji yaro yana da wata d'aya kachal a duniya.

Atsakiyar dare, Rudda ya nemeta tak'i yarda ya rufe ta da duka sai dukanta yake tana ihu, duk yawan matan gida da gayya 'ya'yansu ba wanda yakawo mata dauki.

"Da Rudda ya gaji da dukanta sai kawai ya shak'e mata wuya sai kakarin mutuwa take, gani zai kasheta abanza yasa tashiga lallu6e abinda za ta kwace kanta da shi, cikin sa'a ta ci karo da wuk'a daure a k'ugunsa cikin zafin nama ta zaro ta cikin kube, ba tare da dogon tunani ba ta da6a masa a ciki.

"Yafad'i k'asa yana kugi gani yadda jini ke malala yasa ta buga ihu tafice da gudu tanufi dakuna kishiyoyinta, tana neman taimakonsu.

"Gani halin da mijinsu yake ciki suka fara ihu yayin da 'ya'yansu suka rufe Zaituna da dukan mutuwa.

"Allah ya taimaketa ta kwace daga hannunsu ta 6alla da gudu bala'i ta yanki daji, ba ta ko bi takan bakwani yaronta ba wannan shine sanadin zuwanta Nigeria da farko Lagos tafara yadda zango ana ta hadu da k'awarta Dijama suna aikin wanke-wanke wurin wata bayarba mai siyarda abinci.

"Gani yadda Zaituna take da kyau da diri yasa maza suka fara nemanta da lalata, da farko ta k'i amincewa saida Dijama tai mata huduba sannan ta amince.

"Sannu-sannu idanunsu yana bud'ewa suna k'ara wayewa, da tafiya tai nisa sai suka koma gidan karuwai suka kama d'aki.

"Cikin lokaci k'alilan Zaituna ta zama k'ursugumar karuwa.

Shekaru sun tafi customers suka fara yi musu wuya, sai suka yi kaura zuwa garin kaduna anan ta hadu da Alhaji sambo ya nuna yana sonta da aure nan take ta amince.

"Dijama ta nemo wani malami ya zama waliyin Zaituna aka daure musu aure ta tare gidan mijinta Alhaji sambo, anata gajere tunani tun da tafi uwargida Alhaji kyau nesa ba kusa ba dole ita ce mowar gida.

Da yake Uwargidan Alhaji Sambo ita ma ba kanwa lasa bace, ta tsare gaba ta tsare baya shi kanshi Alhaji tsoronta yake saboda bata bar shi a banza ba.

"Zama yak'i dad'i tsakani Zaituna da kishiyarta, ita da kanta tanemi Alhaji Sambo yasaketa saida suka kai ruwa rana kafin ya amince yasaketa d'in.
Bayan ta kashe aureta da Alhaji Sambo ta ji ba za ta iya komawa, k'azamar sana'arta ta karuwanci ba ta ja jari da kud'in da take tarawa a asusunta na banki.
Ta shiga safarar tufafi na mata da na zama daga Dubai, gani haka yasa k'awarta Dijama ta watsarda karuwanci ta aure wani Alhaji Yusuf da ke zaune a garin Abuja, wannan shine dalilin Zaituna na sake kaura zuwa babban birnin tarayya Abuja tanemi gida a unguwar Garki ta kama hayya.
"Yayin da mijin Dijama ya bata jari mai kauri ta zuba a kasuwancin Zaituna, cikin d'an lokaci kad'an suka bud'e manya shaguna har guda biyu.
Lokaci ya mik'a sosai har Dijama ta kai ga haihuwa, wannan ne ya sakawa Zaituna tunanin sake yin aure kwatsan Allah ya had'ata da Suraj Ardo, da farko ya nuna zai aure ta ko ya akayi auren ya juye kan d'an uwanshi Muhammad, Alhaji Muhammad Ardo aminine awurin mijin Dijama.
"Batare da dogon bincike ba ido rufe da zugar Suraj Alhaji Muhammad ya aure Zaituna, irin aurenan na bariki.
Da yake uwargidansa Maryam mace ce mai hak'uri gaske da kauda kai sai zaman nasu ya yi dad'i.
"Wata Zaituna biyu a gidan tasami ciki, ashe ita ma Maryam tana da shi 6oyewa ne kawai ta yi batare da tafad'awa kowa ba.
'Sa6ani Zaituna da gaba d'aya dangin mijinta ba wanda baisan tana da ciki ba, farin ciki awurin Alhaji Muhammad ba kama hannun yaro.
"Cikin maryam yana da wata hudu ya bayyana saboda tsananin girmansa, sai lokaci Muhammad yasan tana da ciki ranar kamar zai yi hauka saboda murna da farin ciki.
"Gaba d'aya kulawarsa da tattalinsa suka koma kan Maryam, hakan ba k'aramin bak'antawa Zaituna ya yi ba.
"Cikin Maryam na da watani shidda ta had'u da lalura ta6in hankali, duk wani asibiti na masu ta6in hankali, Muhammad yakaita abin yaci turo dama ciwo ke shiga farat d'aya sauki kuma ya na zuwa ahankali.

"Rayuwar Maryam gwanin ban tausayi ga ciki ga hauka, ko yaushe k'ok'arin take ta gudu, ba yadda dangin Muhammad ba su yi da shi ba akan yakai Maryam Mental asylum amma yak'i amincewar da shawararsu.
Aganinshi Maryam bata chanchanci hakan daga gareshi ba, ya tabbata da shine ya had'u da lalura irinta ta ba za ta gujeshi ba.
Za ta zauna da shi har k'arshen rayuwarta saboda haka ya za6i zai cigaba da zama da ita har zuwa lokaci da Allah zai bata lafiya.
"Gani halin da Maryam ta tsince kanta aciki yasa Zaituna ta yi laushi, tagano rayuwar d'an adam ba'a baki komai take ba.
Tadawo tana bata kulawa ta musanmman duk da kowace daga cikinsu cikinta ya tsufa, wani ikon Allah rana d'aya suka haihu Zaituna ta haihu da safe d'a namiji kyakyawan gaske.
"Yayin da dare na zagayowa Maryam ta haifi 'ya mace saidai bata zo da rai ba, ranar Muhammad har kuka sai da ya yi ranar sunna d'a Zaituna ya zagayo aka saka masa Aliyu.

Daga lokaci haihuwa ta budewa Zaituna ta haifi Zainab, shekarar Zainab biyu kachal ta haifi Amina sai auta Fatima.
"Fatima tana fama da lalura ta shafar jinni tun tana yarinya take fama da ciwon wanda har zuwa yanzu ana nema mata magani duk tsawon wannan lokaci Zaituna ba ta waiwayin K'asarsu Nijar ba.
******------*****-----

Family Alhaji Usman Barkido family ne mai girman gaske, wanda girmansa yasa duk wanda yake cikin garin Adamawa yasan da wannan family kasancewarsu jinin sarauta.
"Alhaji Usman Barkido yana da 'ya'ya da tarin jikoki, saidai duk yawan 'ya'yanshi bai yarda sun yi aure ba daga  daga tsatso shi ba, don haka tun daga kan 'ya'yanshi mata har zuwa maza aure had'i yake musu.
"Wannan al'ada ta shi hatta jikokinshi ba su tsira ba, namiji ko mace da kai isa aure zai nemo maka partner kuma, kuma cikin amincewa Allah sai ka ga sun zauna lafiya.
"Barrister Amina Abdallah Barkido tana d'aya daga cikin jikokinsh 'ya ce ga d'ansa Abdallah Barkido.
Abdallah Barkido mutum ne mai tsautsura ra'ayi mafad'aci gaske mutum ne mai zafin rai, matarshi ta aure d'aya Hindu shi da Hindu anyi musu aure had'i batare da su na son juna ba.
"Abdallah baya son Hindu ko kad'an duk da kasancewarta kyakyawa aji farko, kuma 'yar uwarshi ta jini hakan bai sa ya so ta ba.
"Hindu mace ce mai hak'uri gaske duk wulak'anci da Abdallah yake mata shanyewa take, bata kai k'ararsa ba Allah yabata cikinta na fari ta haifi Amina wacce suna mahaifiyar Abdallah ta ci shiyasa suke kiranta da Minal.
"Zuwan Minal duniya ya chanza Abdallah har yafara nunawa Hindu k'auna.
Abdallah yana matuk'ar son Minal bai had'ata da komai ba, lokaci da tana yarinya idan tana rashin lafiya har kuka yake yi.
Muddin kanaso ka ga 6acin ransa kata6a Minal.
"Shekarar Minal biyu a duniya Hindu tasake haihuwa 'yan biyu duka maza, Khalil da Khalid sai Ahmad sai kuma auta Rahma wacce bata wuce 9yrs ba.
"Minal lawyer ce mai zaman kanta sau biyu Barkido yana za6a mata miji tana rejected, tare da goyon bayan mahaifinta Abdallah wanda yasha al'washi ba zai ta6a bari ayiwa 'yarshi auren dole ba.
"Wata rana Alhaji Muhammad Ardo yakawo ziyara a yola, ya je gaida Barkido kasancewar Barkido abokin margayi Aliyu Ardo ne.
Anan yake tambayarshi Aliyu yaranshi nawa, sai ya ce har yanzu bai yi aure ba, sosai Barkido yarufe Muhammad da fad'a daga k'arshe ya ce ya turoshi ya zo ya ga Amina su dai-daita.
*wannan kenan*
[7/26, 11:38 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBEN WANNAN NUMBER*
0813943903

*GIDAN RINA*

*Haske writers association*

Na Jeeddah Aliyu

*4*

*CIGABAN LABARI*

Barrister Amina tana tafiya tana tunanin maganganun da Barrister Zarah, ta gaya mata wanda suka zama sanadin rage mata damuwa.
"Agajiye ta iso gida a parlour ta tararda mahaifiyarta Hindu wacce suke kira da Ummi suna zaune da Rahma, da ke kallon cartoons.

Da sallama dauke da bakinta tashigo.

Sannu da zuwa Ya Minal.
Rahma tafad'a tana mai mik'ewa tsaye ta kar6i handbag din Minal
Yauwa Rahma kallo ake yi?"
Eh! Cewar Rahma tana mai nufar dak'in Minal takai mata bag d'in.
"Washhh! Barrister A tafad'a had'e da zama akan hannun kujerar da Ummi ta ke zaune.
"Sannu da gida ummi?"

"Yauwa Minal sannu da zuwa ya aiki da fatar anyi nasara?"

Alhamdulillah!
cikin yarda ubangiji mu yi winning case d'in.
masha Allah!
Ummi tafad'a cike da farin ciki nasara 'yarta ta.
Mik'ewa ta yi had'e da furta Ummi bara na watsa ruwa ko na d'an ji k'arfin jikina.
Toh! Afito lafiya
ummi tafad'a da murmushi akan fuskarta.
Da isar ta d'akinta ta cire kayan jikinta ta daura towel, ta fad'a bathroom ta sakewa kanta shower bata dauki dogon lokaci ba tafito, ta zauna gaban mirror ta shiga shafe lallausar fatar jikinta da lotion mai k'amshi gaske.
"Ta gyara fuskarta ta hanyar simple makeup, ta bud'e closet tafito da gown na atamfar Holland tasaka had'e da fesa Arabia perfume ta jikinta dauki k'amshi.
"Rahma ta turo k'ofa dauke da sallama.

Ya akayi ne auta?"
Ummi ta ce in gaya miki in kin kammalla abinda ki ke tana son ganinki.
"Ta kalli k'anwarta ta anatse ta ce ki ce da ita gani nan zuwa.
Toh!
Rahma tafad'a tana ficewa daga d'akin.
Barrister A ta cigaba da daura d'an kwalinta tana kammalawa tafice rik'e da wayoyinta.
Tana isa parlour ta tararda ummi tana waya, ta samu wuri ta zauna, tana karantar yanayinta koda wata damuwa sai taga sa6anin haka, sai ma fara'a takeyi.

"Ummi ta k'are wayar ta juyo ta kalli Barrister A fara'a tak'ara yalwanta akan fuskarta, ta ce dama zan yi miki magana akan mutane da za su zo neman aurenki.

"Ummi ta yi shiru na wasu 'yan dak'ik'u kafin ta ce shine naga yadace mu yi magana.

Toh.....ummi ina saurarenki.
Cewar Barrister A tana mai gyara zamanta.
Yayin da Ummi ta cigaba da cewa Minal lokaci yana tafiya a kullum k'ara girma ki ke, shekaru ki suna tafiya ak'allan yanzu kina da shekara 25 a duniya zuwa wannan lokaci ya kamata ace kina d'akin mijinki.

"Amma a dalilin taurin kanki da na mahaifiki gashi har yanzu kina gida, Minal ki yi wa kanki fad'a kada ki biyewa mahaifinki da ke cewa ba zai miki auren dole ba.

"Daga ni har shi aure zumunta akanyi mana gashinan muna zaune har aka haifeku.
Don haka ina gargad'inki a wannan karon ki amince da za6in da Barkido ya yi miki na tabbata ba zai miki za6en tumu dare ba.

"Sassanyar ajiyar zuciya Barrister A ta yi jikinta ya yi sanyi magangganun Ummi suka ratsa ta tabbas zance Ummi gaskiya ne shekarunta sun tafi, ita kanta tana yi so aure saidai sam batason aurenan na Zumunta saidai a wannan karon tana jin za ta amince da za6in Barkido, kasancewar za6i nasa ba daga family su bane.

"Minal kin yi shiru ba ki ce komai ba.
Ummi ta katse mata zance zuci.
murmushi ta yi ta rik'o hannun Ummi cikin nata ta ce Ummi please ki daina sanya damuwa akaina shi aure lokaci ne da shi, auren zumunci ne banaso Ummi amma tun da wannan ba daga Barkido family ya ke ba na amince zan aure shi.

"Alhamdullih!
Ummi tafad'a very excited ta rungumo Barrister A zuwa jikinta daga bisani ta ce in Abbanki ya dawo ya tambaye ki, kin amince da Za6in Barkido ki fad'a masa kin amince za ki aure shi kinji My dear?"

Dariya Barrister A ta yi had'e da cewa kai Ummi.
Shafa fuskarta Ummi ta yi tana tayata dariyar, ta ce kinsan halin botsarare mahaifinki sai da haka akanki da kowa zai iya 6atawa banaso a dalilinki yasamu sa6ani da mahaifinshi, musanmman da yanzu Barkido ya tsofa abu kad'an zai iya mayar da shi babba.

"Karki damu Ummi wallahi na amince da ko ma waye d'ari bisa d'ari.
Allah....ya yi miki albarka yasa biyayyar da ki ke mana ta zame miki alkhairi.

"Amin!
Ummi.
Daga haka su ka cigaba da fira duk dai akan zance auren nata ne.

***----***----*****

Alhaji Muhammad Ardo ya na isowa garin Yola direct Ardo Family house ya wuce, anan ya had'u da 'yan uwanshi suka dunguma zuwa gidan Barkido nemawa d'ansu Aliyu auren Barrister Amina wanda nan take Barkido ya tsayar da lokaci nan da watani biyu masu zuwa.

"Sosai Alhaji Muhammad Ardo ya ji dad'i yadda Barkido ya karrama Su da kuma lokaci da ya sanya na bikin.

Duk zance da ake alokaci Alhaji Abdallah kallonsu kawai yake, saboda ya sha al'awashi muddin Barrister A ta ce bataso Aliyu yasan hanyoyin da dama da zai da bi ya hana auren.

*8:37pm*

Alhaji Abdallah yana zaune a parlounshi, ya aika Ummi ta kira shi mishi Barrister A.

Da sallama ta shigo dauke da bakinta.

"Alhaji Abdallah ya amsa mata yana murmushi.

Barka da hutawa Abba.

"Yauwa Minal.

Ta nemi bisa carpet kusa da k'afafunshi ta zauna

Cikin sanyi murya Alhaji Abdallah ya fara magana, Minal na kira ki ne domin na ba ki damar da za mu tattauna akan zance aurenki.

Ya d'an numfasa daga bisani ya cigaba da cewa har ga Allah Minal naso ki fito da wanda ki ke so za6in ranki, duk nasan zan sha matuk'ar wahala kafin Barkido ya amince.

"Amma hakan ya gagara daga gareki duk lokaci da na zo miki da zance, sai ki ce ba ki samu wanda ki ke so ba.

Ba komai yasa nake miki gudun aure zumunta sai irin zaman da mu ka yi da mahaifiyarki, mun sha bak'ar wahala da hak'uri ni da mahaifiyarki ba kad'an kafin mu fara k'aunar junanmu.

"Banaso ki fuskanci irin wannan rayuwar agidan aurenki.

shiyasa koda yaushe addu'a nake Allah ya kawo miki miji wanda ba daga zuri'ar Barkido ba.

Sai gashi Allah ya kar6i addu'a ta, Barkido da kanshi yai miki za6i ba daga zuri'arshi ba.

"Tun daga lokaci da ya gayamin mijin da ya za6a miki farin ciki ya lullu6e ni, saboda nasan wanene Aliyu ba shi wata matsala ko kad'an yana da halaye masu kyau wanda kowane uba nagari yakewa 'yarshi fatan samunshi amatsayin mijin aure.

"Yayin da Alhaji Abdallah ya cigaba da cewa, duk da Barkido ya gama zartarda hukunci har ya kuma sanya lokaci bikinki nan da watani biyu masu zuwa kamar dai yadda ya fad'a tun kafin zuwansu.

"Saboda haka banaso ki tashi hankalinki, nayi magana da mahaifin yaron, ya ce next week zai zo   ku gane ki kwatarda hankalinki idan bai miki ba, nasan ta hanyar da zan biyowa Barkido ya hak'ura batare da rayuka sun 6aci ba

"Murmushi ta yi cike da jin kunya ta, sadda kai k'asa tana wasa da babban yatsar k'afarta.

Jin Shiru ta ya yi yawa yasa Abba ya d'ago ya kalleta,

shima ya yi murmushi ba ki ce komai ba Minal?"

Idan kuma ba ki da abin cewa za ki iya tafiya.

cikin sanyi murya ta ce Abba ya yi min duk ban ganshi ba, dama ni auren zumunci ne banaso.
"Good girl.....Allah shi yi miki albarka
Amin...Abba.
Tafad'a had'e da mik'ewa tsaye sai da safe Abba zan je na kwanta bacci nake ji.
Allah ya kai mu
cewar Abba.
"Kitchen tafara shiga ta had'a coffee ta wuce da shi zuwa d'akinta.
Gefen gado ta zauna ta yi crossing legs d'inta, ahankali take sipping coffee d'inta.
Yayin da wani gefen na zuciyarta ke nuna ma ta, tayi kuskure na saurin amincewa da mutume da ko sunanshi sai yanzu ta ji.
Tana gama shanye coffee ta wuce bathroom ta wanke bakinta, ta dauko laptop d'inta ta duba wani civil case da za ta yi presenting gobe.
Doguwar hamma ta yi had'e da shafa fuskarta hakan yasa ta rufe laptop d'in ta yi addu'a kwanciya bacci, ta kashe wuta ta kwanta, ta rufe rabin jikinta da blanket.
****----****----***
*WASHE GARI*
*Abuja 11:08am*

Aliyu yafito daga apartment d'inshi jikinshi sanye da white suit, kamar yadda ya saba shigarshi ta farare kaya, wannan yana d'aya daga cikin d'abi'unshi gaba d'aya tufafinshi farara ne.
Baya ta6a saka wani colour kaya idan ba white ba Hannunshi rik'e da brief case cikin yana yin tafiyarshi ta k'asaita ya fito compound, da gudu direbanshi isah ya zo ya kar6i brief case d'in.
shi kuma ya nufi apartment d'in momma zaune ya tararda ita har k'asa ya durku'sa ya gaidata, wannan yana d'aya daga cikin kyawawan d'abi'un Aliyu yana girmama iyayyenshi sosai.
"Momma ta amsa tana fara'a saida ta dube bakin k'ofa ta ga ba kowa, ta gyara zamanta Sultan tun jiya mahaifinka ya dawo daga Yola.
"Uhm! Nasani momma naga lokaci da ya dawo ina tsaye a balcony.
Momma ta d'an yatsina fuska sannan ta ce, ya ce an tsayarda lokaci bikinka watani biyu masu zuwa.
tak'arasa magana cikin murmushin yak'e.
"Ta6e baki ya yi had'e da mik'ewa tsaye momma ni zan wuce office.
Afakace ta galla masa harara, ina magana ka mik'e tsaye kuma ba ka ce da ni komai ba.
"Me Zan ce momma?
Auu.....ba ka da abin cewa?"
D'an bazawari murmushi ya yi momma sauri nake in nadawo za mu yi magana anatse, saidai gaskiya idan har Daddy ya nace akan lalle sai nayi aure to ya barni na nemo wacce nakeso da kaina.
in fact ban shirya yin aure a wannan shekara ba, balle nan da wata biyu ban so Daddy ya yi sauri yanke lokaci biki ba
ahali ni da nake aure ban amince ba.
Rausayar da kai momma ta yi ta ce yanzu kan aikin ga ma ya rika ya gama, ni kaina ban zace zai yanke iri wannan hukunci ba.
Amma ba komai ni ma nasan ta hanyar da zan bulluwa al'amarin.

"Kamar ya momma?"
Ya fad'a da alamar mamaki shinfid'e akan fuskarshi.
wayacewa ta yi ta hanya cewa je ki kawai kada na 6ata maka lokaci kamar yadda ka ce in ka dawo za mu k'arasa
magana.
"Batare da yasake magana ba ya juya ya nufi sitting room d'in Daddy.

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:42 PM] Jiddah Aliyu: *GIDAN RINA*

Na Jeeddah Aliyu

Free page

*Haske writers association*

*5*

Yana had'a ido da Daddy yafara murmushi yana sosa k'eya alamar rashin gaskiya, dariya Daddy ya yi ya ce lale marhaban da bak'on Scotland barka da zuwa Gadanga k'usar yak'i.
"Dariya ce ta subucewa Aliyu ya rufe bakinshi da tafin hannu, Kallonshi Daddy yake yana girgiza kai "Good morning Daddy Aliyu yafada yana shafar gemunshi, Morning Sultan idonka kenan sometimes da sultan Daddy yake kiranshi kasancewar sunan mahaifinshi da yake da, murmushi ya yi yace Daddy am sorry.
"Ba komai sultan...Daddy ya fad'a but zo ka zauna mu yi magana ta fahimta.
zaunawa ya yi kusa Daddy kafin Daddy ya yi magana saida ya rik'o hannunshi d'aya, Sultan dangane da zance aurenka ni da iyayyen yarinyar mu yi fixing din Date nan da watani biyu masu zuwa, saboda muna so ku same isasshe lokaci da za ku fahimce junanku.
"This time around idan ka sake ka ruguza aurenan Sultan I won't forgive you....don haka make sure ka shirya this weekend ka je Yola ku gana da yarinyar.
Ka ji ko?"
Daddy ya tambayeshi, yana kallon yadda ya 6ata fuska tamkar zai yi kuka ga wani uban gume da yake ta faman shawagi akan face d'inshi, da kyar ya hadiye wasu yawu sakamako bakinshi da ya bushe ya ce Daddy please.....idan har ya zama dole sai nayi aure ina neman alfarma ka ba ni dama na nemo wacce nakeso, Saboda ba lalle bane kanemo min kalar mace da nakeso ba...
Shut up....my friend!
Daddy ya daka mishi tsawa wallahi sultan ka shiga taitayinka da ni, muddin ka ga ba'a yi aurenan ba k'addara hakan amatsayin bana numfashi tashi maza ka 6ace min da gani, shassha banza da wofi.
K'asa da murya Aliyu ya yi ya ce Daddy am so sorry karka yi fushi da ni please.....duk abinda ka ke so zan yi saboda ba zan iya jure fushinka ba.
"Dauke fuska Daddy ya yi da barin kallonshi, hakan yakara rud'a Aliyu ya durkusa agabanshi,

Daddy nace na amince muddin zan sanyaka farin ciki koda mayya ce zan aureta.
Sai lokaci Daddy ya saki fuskarshi ya ce that's my boy.....saidai ba mayya ba ce jikar Barkido ce sunanta Barrister Amina 'yar manyan mutane ce shiyasa banaso asame matsala, daga bangare na.
"Zaro idanu Aliyu ya yi hade da Squeezing face.....Daddy kana nufi yarinya lawyer ce?"
Kwarai kuwa independent lawyer ce[lauya mai zaman kanta]
Whatever! Daddy ni ko lawyer government ce I don't care kawai dai kasan I hate liar's kuma mostly lawyers mak'aryata ne, hararrashi Daddy ya yi had'e da furta banaso shirme Gadanga don kawai tana lawyer shi zai sa ta zama mak'aryyarci?"
"Turo baki ya yi a sangarce ya ce ni dai Daddy I don't love her.
mak'e kafad'a Daddy ya yi irin I don't care dinan, kafin ya ce kai dai karka yi gaggawa ka jira har ka ganta ido da ido.
Mik'ewa Aliyu ya yi Sai na dawo Daddy ina da meeting around 12 o'clock.
asauka lafiya....Daddy ya fada da murmurshi akan fuskarshi.
Ficewa ya yi yana fitowa isah direba ya jawo mota ya bud'e mishi back sit ya kame a owners corner, isah ya ja motar cikin kwarewa da tuk'i ya fice daga gidan.
****--*****-----****
Sai around 2:20pm Aliyu ya fito daga conference hall, kaitsaye office d'inshi ya wuce ya ajiye laptop dinshi da wasu files akan desk ya wuce ya bathroom ya dauro alwala, yana fitowa P.A shi Kamal na shigowa rik'e da white coat d'in Aliyu yanufi wata hanger da ke ajiye a cikin office d'in ya sarkafe rigar.
"Aliyu yana fitowa daga bathroom da
sauri kamal ya shinfid'a mishi praymat
Batare da Aliyu ya kalle shi ba ya ce Kamal ka yi min order food a chicken republic restaurant, yunwa nake ji cikina sai k'ugin yake.
"An gama Boss!
Har kamal ya juya ya sake cewa ba ka ji ba kamal.
Chak...kamal ya tsaya.
"please help me call Jamal tell him I wants to seen him urgently.
Yes boss!
Cewar kamal yana mai ficewa daga office din.
Aliyu yana gama sallah ya koma kan resting chair ya kwanta, ba abinda yake tunawa sai babban k'alubali da yake tunk'aro shi, duk duniya ba abinda ya tsana irin aure duk yadda ka ke da shi idan ka yi invited nashi daurin aure ba ya zuwa, ko a family su ake aure sai ya k'irk'iro tafiya don kada ya je sosai abin yake ciwa Daddy tuwo a kwarya.
"Mtsss....ya ja d'an siriri tsaki ya dafe goshinshi duk lokaci da ya tuna Daddy ya ce dole sai ya je Yola wurin yarinyanan, sai ya ji fad'uwar gaba wanda ya rasa na menene babban tashin hankalinshi bai san yadda zai ga yarinyar ba, ko yaya take bashi da mafita dole ya aureta don ya farantawa mahaifinshi rai.
"Turo k'ofar da aka yi ya katse mishi tunani da sallama kamal yak'araso, kusa da Aliyu ya ajiye ledar hannunshi.
"Boss na kira maigida Jamal ya ce zai zo nan ba da jimawa ba.
Okay.....ba damuwa za ka iya tafiya.

Ficewa kamal ya yi yayin da Aliyu ya dauki takeaway guda yafara ci kasancewar yana jin yunwa yasa yaci fiyye da rabin abincin.

"Abinci yake ci amma zuciyarshi cike da zance zuci, turo k'ofar da aka yi ya katse mishi zance zuci da ya ke yi, sallamar Jamal ta bugi dodon kunnenshi, ya dubi k'ofar yana mai amsawa Jamal ya shigo ya zauna kusa da Aliyu yana mai mik'a masa hannnu suka yi musabaha.

"Ya garin JB kwana biyu ka 6oye?"

Aliyu ya fad'a yana kallon fuskar Jamal.

Alhmdllh....kwana biyu nan am too busy tun lokaci da Abba ya yi rashin lafiya abubuwa su ka min yawa.

"Sauke numfashi Aliyu ya yi kafin ya ce gaskiya iyayyenmu suna bukatar hutu musanmman yanzu da k'arfi kullum k'ara ragewa yake, gara kai JB kana da siblings maza su na taimaka maka a business d'inku sa6ani ni da bani da kowa

"Ta6e baki Jamal ya yi kafin ya ce kadai ayi sha'ani kawai amma lamarin 'yan uwan nawa sai addu'a daga mai shaye-shaye sai manemi mata, shiyasa kullum jini Abba k'ara hawa yake.

Girgiza kai Aliyu ya yi ya ce Allah ya kyauta ya shige mana gaba.

Amin summa Amin!

cewar Jamal yana mai daukar robar ruwan Faro ya bude, ya kafa baki ya sha daga bisani ya ajiye.

Ya dube Aliyu ya ce king ya zance da mu ka yi a waya yanan ko ka watse shi?"

Yak'arasa magana yana dariya.

Uhm! Bari kawai JB wannan karo zance ba zai watsu ba.

Yanzu haka neman da nake maka zance nakeso, mu tattauna akai.

"Daddy ya ce na shirya ranar Saturday naje naga yarinyar, sai ka shirya mu tafi tare.

"Allah yakaimu cewar Jamal.

Cigaba da tattauna zance suka yi.

****----*****-----*****

Yammacin ranar Juma'a Barrister Amina tana zaune a office d'inta black suit ne sanye ajikinta, ga farin gilashi d'inta da ta manna a fuskarta ya yi matuk'ar fitowa da kwarjininta.

Ta tattara hankalinta akan system, aka yi knocking k'ofa, yes.... come in.

Tafad'a tana mai cigaba da aikinta aka turo k'ofa tare da sallama ta amsa batare da ta d'ago kanta ba, ta ce bebs sai yanzu ki ka fito?"

Uhm....bari kedai bebs case din yau ya bani kashi ba kadan ba kinsan shegen iyamuri nan Barrister Obi shi ne  defendant lawyer, yanzu dai an d'age zama sai on 16 za'a cigaba da saurare k'arar.

"Hmm!

Barrister Amina ta yi ajiyar zuciya had'e da cewa karki damu bebs insha Allah za ki yi nasara, Allah yana tare da ma su gaskiya.

"Haka ne bebs thanks for the courage me.

You're welcome!

Suka yi shiru na few seconds daga bisani Barrister Amina ta kawo karshen shiru nasu ta hanyar cewa, bebs kamar yadda ki ka bani shawara na yi istahara akan mutume nan na yi, ba zan 6oye miki ba bebs akwananki nan kullum sai nayi mummunan mafalki wanda na rasa gane me hakan yake nufi.

*DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:44 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

Na Jeeddah Aliyu

Free page

*6*

Ajiyar  zuciya Barrister Zarah ta yi ta gyara zamanta, ta fuskanci Barrister Amina ta ce ki kwatarda hankalinki bebs insha Allah ba abinda zai faru sai alkhairi, ke dai ki cigaba da addu'a zan kuma je waje Malam(tana nufi kakanta da ya haifi mamanta) ya taimaka miki da addu'a.
"Numfashi Barrister Amina ta sauke kafin ta ce gashi gobe ne ranar zuwanshi, zuciyata cike take da fargaba had'uwa da shi.
"Murmushi Zarah ta yi ta ce kidaina fargaba bebs, insha Allahu alkhairi ne zai biyo baya.
Allah yasa.
Cewar Amina.
***----***----****
*8:34pm*

Aliyu na zaune a falonshi yana duba wasu documents na wani project da yake yi, Zee-zee ta yi sallama ta shigo ya amsa tare da d'agowa ya dubeta sanye take da 'yar fingilalliyar riga wacce ta wuce gwiwarta, kanta ba d'an kwali ta gyara gashi ta sai kyalli yake.
"Ya Ali momma ta ce ka zo tana so ganinka.
Mtsss.....ya ja tsaki cikin hargowa ya ce wai Zainab meke damunki ne?"
wannan wacce irin banzar shiga ce?"
Dube yadda ki ka fito tun daga apartment d'inku har zuwa nan, baya kinsan gidanan cike yake da maza wanda ba muharamanki ba.
"Ya motsa fuska Zee-zee ta yi tana wani turo baki, yi hak'uri Yaya Momma ce ta azalzale ni akan lalle sai nazo na kira ka, insha Allahu ba zan sake fitowa a haka ba.
Shikenan je ki ki ce mata ina zuwa.

Ficewa ta yi yayin da ya shiga tattara takardu da ya zube akan carpet, sannan ya fice a falo ya tararda momma ta hard'e akan sofa.
"Barka da hutawa momma!
Yafad'a had'e da zaunawa akan kujera da ke facing d'inta.
Shin da gaske ka amince da za6in mahaifinka, kuma gobe za ka tafi Yola ka gana da ita?"
Gyara zama ya yi kafin ya ce Eh....haka ne har nayi magana da Jamal zai rakani, morning flight za mu bi saboda mu dawo da wuri.
Har ya dasa aya azancenshi tana mishi kallon k'asan ido, wanda ke nuna mamakinta a 6oye.
"Sultan!
Ta kira sunanshi tana mai sauke kwayar, idanunta akan fuskarshi
Na'am momma!
"Ba na gayamaka kada ka amince da aurenan ba, da yake ka fi so farin ciki mahaifinka akaina shine ka amince ko?"
Girgiza kai ya shiga yi Allah momma ba haka bane daga ke har shi inaso farin cikinku, na amince da aure ne ba don raina yana so ba sai don na farantawa Daddy rai.
Amma wallahi momma babu son aure ko k'ank'ani a zuciyata, bana kuma tunani ko da anyi aure zan sauya ra'ayina.
"Sai anan gaba za ka gane kuskure da ka yi na amicewa da aurenan.
Momma....please karki k'aramin damuwa akan wacce nake ciki sanin kanki ne banso aurenan ko sunanshi naji an fad'a sai gaba na yafad'i to miyasa za ki d'aga hankalinki?"
Aure dole ne banaso ayi ma Sultan, shiyasa ka ga na shiga damuwa amma tun da ba ka ciki damuwa Shikenan Allah yasanya alkhairi.
Amin!
Yafad'a had'e da mik'ewa momma ni zan koma ciki akwai aikin da nakeso na k'arasa.
Bai jira jin ta bakinta ya juya ya fice ta bi wani irin kallo mai wuyar fassarawa, daga bisani ta yi kwafa.
***---***-****---****
*YOLA*
*10:07am*
Da sanyi safiyar assabar Barr Amina na kwance akan gadonta, ta k'uddudune cikin wani lallausan blanket barci take yi cikin natsuwa da kwanciyar hankali musanmman, kasancewar yau bata zuwa court shiyasa ta baje abinta tana sauke gajiya.
"Ummi ta turo k'ofar d'akin, ganin Amina kwance yasa ta d'an girgiza kai tare da duba wall clock wanda ya nuna k'arfe 10:07am.
Matsawa tayi gaban gadon ta yaye blanket d'in jikinta ta shiga girgiza ta had'e da kiran sunanta Minal......Minal! Ki tashi hakanan mana ko kin manta yau za ki bak'o ne?"
Omg....!
Tafad'a cikin magagin barci.
Bubbuga k'arfata Ummi tayi ta bud'e idanu da kyar ta kalli Ummi, sannan ta tashi zaune tana murtsike idanuwanta masu cike da zallan barci, a sanyaye ta ce Ummi ki barni nayi barcina ki fad'awa Asabe ta shirya masa meals.
Tak'arasa magana had'e da yin doguwar hamma, alamar barci bai isheta ba.
"Harararta Ummi tayi kafin ta ce banaso shirme Minal ki tashi maza Asabe za ta tayaki da

wasu ayyuka, ba wai ki sakar mata aikin duka ba.
"Yatsina fuska tayi kamar za tayi kuka ta zuro k'afafunta k'asa farare tass....da su, tayi mik'a gani hakan yasa Ummi ta nufi k'ofar fita tana mai k'ara jadadda mata tafito yanzu nan.
"Ummi na ficewa tasake komawa ta kwanta zuciyarta cike da tunani tafara described d'in Aliyu, gajere ne bak'i mai k'ato ciki hancinshi chan sama, da sauri ta tashi zaune tana zaro idanu daga bisani ta girgiza kanta dogon bak'in gashinta ya warwatsu akan gadon bayanta, hannunta tasaka ta tattare shi ta dauko d'an k'aramin band k'ark'ashin pillow ta daure gashin, murmushi tayi had'e da d'an dukan k'eyarta.
"Akaro na biyu tasake zuro k'afafuwanta k'asa ta sauko daga bisan gado 'yar yaloluwar rigar barcinta light pink a bayana, bathroom ta wuce ta bata dauki dogon lokaci ba tafito daure da towel hannunta rik'e da rigar da tacire ta jefata cikin laundry basket.
"Agauggauce ta shafa mai had'e da zura fitted gown na shaking material, bata daura d'an kwali ba sai tasaka hula irin na yadin hijab ta fice.
kaitsaye kitchen ta wuce Asabe ta samu tana had'a plate da spoons d'in da za'a yi breakfast.
"Ina kwana lauya?"
cewar Asabe har da d'an runsunawa.
Lafiya qalau Asabe...antashi lafiya?"
Lafiya qalau lauya.
Asabe Yau zan yi bak'o me kike gani za'a shirya masa wanda ya kamata?"
"Cikin murmushi Asabe ta ce Minal kenan ya za'a yi nasan abinda yake so amma me kike tunanin ya kamata ayi masa, shi kadai ne ko suna da yawa?"
Ta6e baki Minal tayi kafin ta ce wannan ne ban sani ba, kawai mu shirya abinda ya kamata.
Bari nafara fiddo kaji a freezer kafin ki k'arasa naki aiki.
Ta juya tanufi wajen freezer yayin da Asabe ta cigaba da aikinta.
***----****---****
*ABUJA*
*11:24am*

Aliyu yafito cikin shirinsa cikin farare kaya as usual, farar shadda gezner tana walkiya da daukar ido takalmin k'afarshi cover ne suma farare, yayin da ya lullu6e kwayar idonsa da farin eyes glass wanda ake iya hango brown eye balls d'inshi, Jikinshi na fitarda fitinane k'amshi.
kaitsaye falon momma ya wuce gani bata falon yasa ya nufi bedroom d'inta, ya tura k'ofa ya shiga tana zaune gefen gado sanye da cotton night gown, tana waya ganinshi yasa ta katse waya tana wuk'i-wuk'i da idanu kamar marar gaskiya.
"Da murmushi akan fuskarshi ya zauna kusa da ita ya aza kanshi akan shoulder ta, cikin shagwa6a ya ce momma na fito ki yi min addu'a.
Ya motsa fuska ta yi kafin ta ce Allah ya kiyayye hanya, yasa yarinyar tayi maka.
"Kai momma wannan addu'a duk ni kadai?"
"Eh mana yaron momma ko tayi kad'an ne na k'ara ma da wata?
A'a....momma ta yi ta farkon zan amsa miki da Amin.
Ta biyu ce ba zan amsa ba.
"Dad'i ne ya lullu6e momma tasaki dariya har Aliyu yafice daga bathroom din tana dariya.
"Sitting room d'in Daddy ya nufa Daddy na zaune da newspaper a hannunshi yana dubawa,

shigowa Aliyu yasa ya ajiye newspaper d'in ya tattara hankalinshi akan Aliyu.
"Ina kwana Daddy?"
Cewar Aliyu yana mai runsunawa.
"Lafiya qalau Sultan hope shirin tafiya Yola ne.
yana magana yana nuna kayan jiki Aliyu da yatsanshi.
"Eh.....Daddy sallama na zo nayi maka.
Madallah.....Allah ya kai ku lafiya, ka kuma kiyayye banaso a sami matsala daga gareka ka ji ko?"
"Na ji Daddy insha Allahu zan kiyayye.
Shikenan je ki Allah ya tsare.
Amin....Daddy.
Daga haka yafice direbanshi Isah yana zaune a mota yana jiran fitowarshi, kafin Isah ya bude masa k'ofar mota har ya budewa kanshi, ya zauna a back sit Isah ya ja mota maigadi ya bude musu gate, Zone 2 suka wuce suka dauki Jamal sannan suka dauki hanyar Nnamdi Azikwe Airport, bata dauki dogon lokaci ba Jirgi yad'aga.
*****-----*****-----****
*YOLA*

Barrister Amina tafito daga wanka daura da towel iya cinyarta, ta nufi wurin mirror ta dauko hand dryer ta jonata a socket ta shiga busar da dogon bak'in gashinta.
"Bayan gashin ya bushe tashiga shafe shi da mayuka gashi kala dabam-dabam katon band tasaka ta daure gashin.
Kafin tafara shafe lallausar fatar jikinta da body lotion yayin da skin d'inta sai glowing yake.
Simple makeup ta yi ta bude closet dinta ta fito da Arabian gown royal blue in colour, mai adon stones sai walki'ya da daukar ido suke.
"Bayan tasaka inner wears ta zura rigar d'an k'aramin red veil ta yi rulling da shi, perfumes na Amani da Azaan ta mulke rigar da shi nan take ta dauki wani mushiriki k'amshi, ta yi tsaye agaban mirror looking herself don gani yadda ta yi kyau yasa tasaki sanyaye murmushi ba yabon kai ba duk d'a namiji mai ingantattaciyar lafiya ya yi arbani dole ya so ni.
"Barrister Amina tafada a k'asan zuciyarta, kai ta girgiza cike da nishadi ta dauki d'aya daga cikin Shoe dinta da ke jere akan shoerank tasaka ahankali tanemi gefen gadon ta zauna, phone d'inta ta dauko ta yi calling Barrister ladan a vidoes call Barrister ladan tana yi picking tasoma yi mata tsiya gani yadda ta yi kyau yayinda Amina sai sakin murmushi take, daga bisani Barrister Ladan tashiga bata good advised, turo k'ofar da aka yi yasa Barrister Amina juyawa Rahma ce tashigo ta ce Ya Minal Ummi ta ce ki fito bak'i sun iso.
"Ras....ras...sauti da ke fita daga k'irjin Barrister Amina kenan har batasan time d'in da ta dafe chest d'inta da hannunta ba.
Da kyar ta hadiye yawu ta ce je ki ki ce ganinan fitowa.
Rahma ta fice barristers Ladan ta ce tashi ki tafi bebs kinsan wani bayaso jira idan sun tafi za mu yi waya, batare da Barrister Amina ta yi magana ba ta katse kiran ta mike tafice daga d'akin

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:46 PM] Jiddah Aliyu: *HASKE WRITERS ASSO.*💡💡

*DA D'UMID'UMINSU...Daga Alk'aluma shida*

_INA MASOYA? YAU GA RANARKU...._

_DADINA DA GOBE SAURIN ZUWA, TABBAS INKAJI KIRA SAMU NE SANNAN IDAN KAJI WANE TO BA BANZA BA,HAKANNE MA YASA SHAHARARRIYAR KUNGIYAR NAN TAKU MAI FARIN JINI MAIYI DOMINKU DOMIN FARANTA ZUK'ATANKU TASAKE ZUWAR MUKU DA MASU D'UMI KUMA HASKAKKUN LITTATTAFAI GUDA SHIDA RERAS WADANDA TAYIWA LAKABI DA,DA  D'UMI D'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDA GARABASA....ME KUKE JIRA? MAZA KU GARZAYA KU NEMI NAKU TUNDA DUMINSU DOMIN FASIHAI HAZIKAI SANNAN MASU NAZARI KAFIN SU RUBUTA SUNE SUKA HADA KARFI DA KARFE DOMIN NISHANTAR DAKU,MASHA ALLAH RIGIJI GABJI DAGA JI KASAN AKWAI MAGANA, MARUBUTAN DA ZASU NISHANTAR DAKU SUN HADAR DA👇🏻_

*JIDDAH ALIYU*👉🏻 _GIDAN RINA_!

_DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR_ *NIDA YAYA HABEEB*  _DA_ *SONKI NE SANADI*

*A'ISHA DANSABO*👉🏻 _BURIN ZUCIYA_!!

_DAGA SHAHARARRIYAR_ _MARUBUCIYAR_ *LAIFIN BOYE*  _DA_ *HURAYYAH*

*KHADIJA AHMAD KDEEY*👉🏻  _DA CIWO A ZUCIYATA!!_

_DAGA SHARARRIYAR_ _MARUBUCIYAR_ *Y'AR* *BABBAN GIDA*  DA *ABU IRFAN*

*RAHMA MUH'MD RUFA'I NALELE*👉🏻 _RAYUWATA_!

_DAGA SHAHARARRIYAR_ _MARUBUCIYAR_ _LITTAFIN_  *LIKITAN ZUCIYA* _DA_ *SAMARIN BANA*

*SLIMZY*👉🏻 _IZZA TA!!_

_DAGA SHARARRIYAR_ _MARUBUCIYAR_ _LITTAFIN_  *ANYI WALKIYA* DA *TAK'ADDAMA* _WANDA YAKE ZUWA MUKU A KYAUTA👌🏽_

*SAFIYYA GALADANCHI* 👉🏻_TANA K'ASA TANA DABO!!!_

_DAGA SHAHARARRIYAR MARUBUCIYAR_ _LITTAFIN_ *RUBUTACCIYAR KADDARA* _WANDA_ _YAKE ZUWA MUKU YANZUN HAKA A_ _KYAUTA... 👌🏽_

*_WANNAN SHI AKE KIRA DA INBAKAYI BAN WURI,KUMA DADIN DADAWA ZAKU SAMU WADANNAN KAYATATTUN LABARAN AKAN FARASHI MAI SAUKI DAIDAI DA ALJIHUNKU KUDAI KAR KU BARI ABAKU LABARI,GANI YA KORI JI,HASKE MAGANIN DUHU,RUBUTUN MU YA BANBANTA DA SAURAN._* *ZASU FARA ZUWA MUKU RANAR SALLAH DA KWANA UKU,  MUN KAI SHI HAKA NE SABODA AZUMI LOKACIN JAJURCEWA GA IBADA, GA DUK ME BUQATA ZAI IYA BIYA YANZU, SAIDAI LOKACI NA ZUWA KAWAI YAGA ABINSA, IDAN KO SAI SALLAR NE MA DUK D'AYA MUDAI MUNA MARABA DA  MASOYAN MUH*

*DAN HAKA GAME BUKATAR SIYAN WAD'ANNAN KAYATATTUN LITTATTAFAI WADANDA MUKA YIMUSU LAKABI DA D'UMID'UMINSU  SHIDA AKAN NAIRA DARI BIYAR KACAL 500 MAISON GUDA DAYA ZE BIYA 200, ME SON 2 ZE BIYA 300 MESON UKU ZE BIYA 350 MESON HUDU 400 MESON BIYAR 450 ME BUK'ATAR DUKA KUMA ZE BIYA 500 KAMAR YANDA MUKA FADA A SAMA. kU TUNTUBEMU KAMAR HAKA*👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻

_FIRST BANK_
3120641551
_SAFIYA MUSA GALADANCI_
_SHEDAR TURA KUDINKA GA WANAN NUMBER_ 👉🏻08103943903

👇🏻👇🏻👇🏻👇🏻
_ZENITH BANK_
2255398727
_AMINA JIBRIL_
_SHAIDAR BIYANKA GA WANAN NUMBER_ 👉🏻08166177830

_IDAN KUMA KATI NE SHIMA ZAKI IYA TURAWA WANAN NUMBER KATIN MTN GA NUMBER KAMAR_ _HAKA:_ 08039424298 SHEDAR BIYAN KATINKA GA 07084161619

Jeeddah Aliyu

*7*

Lokaci da Jirgin su Aliyu ya yi landing uncle Suraj ne ya dauko su daga Airport, akan hanyarsu ta zuwa gidan uncle suke tattauna zance business da yake uncle Suraj shi yake handled din business d'insu na Yola.
Gidan uncle suka fara yadda zango bayan sun huta suka ci abinci had'e da sallar azhr, sannan uncle ya had'a su da direbanshi yakai su gidan Alhaji Abdullah Barkido Misali k'arfe 2:52pm direban da ya dauko Aliyu da Jamal ya Parker mota cikin gidan Abdullah Barkido, Khalid ne yafito ya tarbe su had'e da yi musu jagaro zuwa falon bak'i.
"Jamal ne yafara zaunawa yayin da Khalid ya fice.
Ahankali Aliyu yake nazarin falon kafin ya zauna yana shak'ar Air freshener & odour neutralizer

din da aka sanyawa, falon sosai ya yi masa dad'i sanyayyar ajiyar zuciya ya yi, sannan ya d'an sosa gefen kuncinshi da yatsanshi, zuciyarshi ta afka tunanin saboda bai san yadda zai ga yarinyar ba, ko yaya kamanunta suke bashi da mafita dole ya aureta domin ya farantawa Daddy rai.

'Tunaninshi ya katse sakamakon sallamar da ta bugi dodon kunnenshi, alokaci d'aya shi da Jamal suka dubi k'ofa Asabe mai aiki ce tare da Rahma suka shigo dauke da kayan abinci, had'e da drinks Jamal ne ya amsa musu sallama, sai da suka ajiye kayan sannan suka gaida su nan ma Jamal ne amsa saboda Aliyu bakinshi ne kadai ya motsa ko Jamal da ke zaune kusa da shi ba lalle bane ya ji abinda ya ce ba.

"Bayan Asabe ta bar falon Rahma ta ja tai tsaye tana kallonsu, Jamal ya ce Baby ya sunanki?"

kusa da shi ta nufa da yake Rahma akwai d'an banza surutu kamar parrot ta ce sunana Rahma Abdallah Barkido, kaine za ka aure Ya Minal ko wannan da baya magana?"

Takarasa magana had'e da nuna Aliyu da baki.

"Aliyu ya d'ago fuskarshi dauke da lallausan murmushi, da yake sosai maganar Rahma ta bashi dariya shiyasa ya murmusa, Jamal ya yi 'yar dariya ya ce bani bane wannan ne ya nuna Aliyu da yatsa.

"hannunta Aliyu ya rik'o yana murmushi ya ce Rahma yakike ya karatu?"

Lafiya qalau....kaine za ka dauke mana Ya Minal?"

"Gyad'a mata kanshi ya yi yana cool smile ko ba za ki barni na dauke ta ba?"

Turo baki ta yi kafin ta ce zan bar ka saboda kana da kyau amma duk da haka saidai katafi da mu duka gidanka.

Jamal ya kyalkyale da dariya yayin da Aliyu yak'ara fad'ad'a murmushinsa har kana iya jiyo sautinsa ya ce na amince Baby Rahma, ya zura hannu cikin pocket dinshi ya fito da bundle na 'yan five hundred ya mik'a mata gashi Baby Rahma tasha ice cream.

"Girgiza kai ta yi ba zan kar6a ba Ya minal za ta dokeni, haka ranar abokin aikinta ya zo ya bani kudi na kar6a bayan ya tafi ta zane ni.

"Kwatarda murya Aliyu ya yi ya ce kar6i kawai ba zan barta ta dokeki ba, kinmanta ni ne zan aureta?"

Washe hak'ora Rahma ta yi tasaka hannu biyu ta kar6i kudi ta yi mishi godiya ta fice da gudu tana murna.

"Bayan fitar Rahma Jamal ya dubi Aliyu ya ce duk da ak'oshe mu ke amma yakamata mu ci koda snacks ne da drinks gudu kada su ji babu dad'i.

Uhmm.....Aliyu ya fad'a had'e da daukar samosa guda d'aya ya kuma tsiyaya Juice a handle glass cup, yana kur6a juice d'in a hankali.

Sautin tafiyar takalminta ne yafara isa musu da sak'on zuwanta, kafin ta tura k'ofar falon ta shigo k'amshinta ya mamaye k'ofufin hancinsu, cikin sanyayeyar muryarta mai matukar dad'i da gard'i ta yi sallama.

[7/26, 11:47 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU...DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*

08103943903

*SAI KA TURA SHAIDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*

08166177830

*ZA KI IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYAN KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMIND'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```
*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```
*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA```
*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELE*:-```RAYUWATA```
*SLIMZY*:-```IZZA TA```
*SAFIYA GALADANCHI*:-```TANA K'ASA TANA DABO```

*GIDAN RINA*

*8*

Cikin fara'a Jamal ya amsa mata sallama, sai da ta zauna sannan ta gaida su Jamal ne yasake amsawa yayin da Aliyu yake k'are mata kallo ta k'asan ido.
Jamal ya gyara zamanshi ya ce sunana Jamaludeen Muhammad, tare muka taso da Aliyu tun muna yara ko zan iya sanin sunan amaryar ta mu?
Sai da ta yi lallausan murmushi cikin sweetness voice d'inta ta ce sunana Barrister Amina Abdallah.
Wow! masha Allah ashe amaryar ta mu lawyer ce?"
Uhmm.....tafad'a had'e da sadda kai k'asa.
Da fatar mun samu kar6uwa a wurin Barrister?"
Cewar Jamal yana mai kallonta.
Da kyar ta d'ago saboda kunya kunsan mu fulani da kunya duk wayewar mu da gogewar mu, za ka sami wasu daga cikinmu da kunya....lol.
Ba k'aramin namijin k'ok'ari ta yi ba ta hanyar furta, insha Allahu daga gareni ba bu wata matsala fatana anan Allah ya had'a kawunan mu.
Amin summa Amin Barrister.
Jamal ya fad'a cike da jin dad'i maganarta ya mik'e ya kalli gefen da Aliyu yake zaune ya ce king bari na ba ku wuri ku fahimce juna.
Kafin Aliyu ya yi magana har Jamal ya fice, shiru suka yi na tsawon lokaci yayin da kowane su da abinda yake sak'awa a zuciyarshi.
"Aliyu ya gyara zamanshi ya tattaro hankalinshi gareta sam bai dauka haka zai ganta ba, ya yaba da irin shigar da tayi sai yaji ta burge shi, karo na farko a tarihin rayuwarshi da shigar wata

'ya mace ta burge shi ba ko shakka dole ya rubuta wannan a diary shi.
"Cikin husky voice d'inshi yayin da fuskarshi ke dauke da murmushi, ya ce Barrister Amina ya gida?"
Ta cire kai da kyar ta kalle shi wani irin shock ta ji ya jata, a hankali ta bude baki ta ce "Lafiya qalau, ya hanya da su mommy?"
'Alhamdullah!
Yafad'a yana kallonta suna had'a ido ta yi sauri sadda kai k'asa.
Daddy ya gayamin ke lawyer ce mai zaman kanta, kenan idan mu kayi aure anan za ki zauna ko za ki bi ni Abuja?"
"Sai da ta yi murmushi kafin ta ce duk Inda ka za6a mana.
Ya fad'ad'a murmushinsa har lokaci idanuwanshi na kanta ya ce, gaskiya na fi zama a Abuja da Lagos idan ki amince sai mu zauna a Abuja ko ya ki ka gani?"
"Ba laifi hakan ya yi.
Tafad'a Cikin sanyi murya.
Shikenan Allah ya nuna mana lokaci.
"Da kyar ta iya furta Amin.
Daga haka suka yi shiru.
Aliyu ya sauke ajiyar zuciya ya kalleta dai-dai ita ma ta d'ago ta sace kallon nashi, karaf....suka had'a ido da sauri ya dauke kanshi, jimm....ta yi tana kallon gefen fuskarshi yana juyowa ta kauda kanta.
Ya duba agogon da ke daure a tsintsiyar hannunshi sai ya mik'e tsaye yana cewa mu je ki rakani mu gaisa da Mama.
Ta mik'e tsaye ta wuce gaba yana bin ta, a farfajiyar gidan suka hango Jamal tsaye yana waya, alama Aliyu ya yi mishi da hannunshi.
"Hakan yasa Jamal ya katse wayar ya kuma nufo su, har Falon Ummi ta shigar da su ta ce ku zauna bara na kirata bayan ta kira Ummi suka gaisa sannan suka yi mata sallama har compound ta raka su idan direban uncle ke zaman jiransu.
"Tsaye suka yi suna facing junansu, kafin ya yi magana wayarshi ta yi ringing ya fito da waya gani momma ce mai kiran nashi yasa ya kalli Amina ya ce please  2 minutes.
Uhmm.....Tafad'a tana mai wasa da zoben hannunta.
Nesa da ita ya yi ya amsa wayar, yana receiving ya kara wayar a kunnenshi hello....momma! Ya hanya yaron momma?"
"Alhamdulillah....momma mun iso lafiya har muna shiri wucewa sai ga kiranki.
"Uhmm!
Da fatar yarinyar ta yi maka?"
Murmushi ya yi mai sautin gaske had'e da shafar sumar kanshi, ya ce momma za mu yi magana idan na dawo gida lokaci yana k'urewa kada mu yi missing flight d'inmu.
"Daga haka ya katse kira saboda yasan halinta sarai sai tasake, watsu masa wata tambaya.
Daga chan gefe kuma Barrister Amina ta k'ura masa ido tana nazarinsa daga sama har k'asa, tabbas ya amsa sunanshi cikkake namiji domin ya mallaki komai na cikar halitta, ta d'an namiji wanda kowace lafiyayyar mace za ta yi burin mallakarshi a matsayin life partner.
"Ganin ya juyo gareta yasa ta yi gaggawar kauda kanta, ya k'araso daf da ita shi ma kallonta ya yi sosai sannan ya yi gyaran murya tare da kiran sunanta Aminaaa......!

Yadda ya ja sunanta yasa tsigar jikinta tashi yarrrr.....
Ta d'ago ta kalleshi ya ce mu za mu wuce saboda yau za mu koma Abuja, gashi ban yo miki tsarabar komai ba, sai wani lokaci idan Allah yasake had'a mu.

"Murmushi ta yi wanda yak'ara mata kyau ta ce ba komai, nagode da ziyara Allah yakai ku lafiya, ka gaidamin da su mommy.

"Amin...

Ya furta chan k'asan mak'oshi.

Ta juya wajen Jamal ta ce malam Jamal nagode Allah ya kiyayye hanya ka gaida iyali.

"Mu ke da godiya barrister.

Cewar Jamal.

Daga haka ta juya ta nufi cikin gida.

Yayin da Aliyu da Jamal suka shiga mota direba ya ja aka bude musu gate direct Airports ya kai su, ko gidan Uncle Suraj ba su koma ba.

****---****----****

*ABUJA*

Momma zaune akan sofa abin duniya ya taro ya yi mata yawa, tun jiya da Aliyu ya dawo daga Yola har zuwa yau bai bari ta had'u da shi ba.

Yau tun da sassafe ya fice kuma har yanzu yamma lis bai dawo gida ba, ta kira phone d'inshi yafi a kirga saidai ta ji P.A shi ya dauka ya ce yana meeting.

"Mtss...ta ja tsaki daga bisani ta dauki wayarta ta yi dialling, d'aya daga cikin contacts d'inta sunanshi ya bayyana akan wayarta, kamar haka Jarumi!"

Wayar ta shiga ringing kamar ba za'a dauka ba saboda saida ta yi kusan tsikewa, ya yi picking Hello....

Yafad'a ahankali.

"Cikin rawar murya momma ta ce Jarumi akwai gaggarumar matsala da ke shirin tunk'aro mu, idan har mu ka yi sake ta afku shikenan mafalkinmu ya zo karshe.

"Har ta dasa aya a zance ta Jarumi yana saurareta, huce ya yi ya fesar da iska mai zafi daga bakinshi, cike da tafarfasar zuciya ya ce duk abinda yake faruwa nasani kema kuma kin san nasani, yanzu haka ina cikin garin Abuja domin mu nemowa kanmu mafita.

"Ki zo Ina  westerns dreams hotel room 402, saboda wannan magana ba ta waya bace gudun kada wani ya jiyo ki lokaci da mu ke magana.

Yana gama magana ya katsi kiran.

A gurguje momma ta nufi bedroom d'inta ta shirya key motarta ta dauka had'e da handbag, ta nufi k'ofar fita kicibuss....ta yi da Tima zaune a k'ofar fita daga main parlour ta wargaje gashi kanta, ya rufe mata fuska.

"Gaban momma ya fad'i....rass!

Cikin sark'ewar halshe momma ta ce Ti....Ti...ma me ki ke yi anan?"

Tashi maza ki koma bedroom d'inki.

"Wata mushirika dariya Tima ta yi mai amon gaske ta ce ba Tima ba ce, rijiya ce mai dauke da kunamu da macizai sun lullu6e wata 'yar jakka mai dauke da kundin sirri.

"kafin kyaftawa ido har Tima ta mik'e kamar walk'iya, ta kai k'ofar d'akinta.

Da mugun tsoro momma ta bi ta da kallo, da kyar ta hadiye yawu sakamakon yadda

mak'oshinta ya bushe.
"Har Tima ta kama handle d'in k'ofa ta juyo tasake
Kyalkyalewa da dariya ta ce je ki momma je ki maza kada jirgi ya tashi ya barki ba lalle bane ya dawo daukarki.
"Kafin momma ta yi yunk'uri furta wani abu har Tima ta shige d'akinta.
Mtsss.....!
Momma ta ja tsaki ta girgiza kai tai ficewarta hankali kwance.
Abinda zai ba ka mamaki momma na isa Hotel d'in ta ciro bak'ar jallabiya daga k'asan seat din motarta ta sanya had'e da yane kusan rabin fuskarta, da mayafin rigar, ta ciro wani k'ato black shade ta lullu6e kwayar idonta duk sani da kayi mata ba za ka gane ta ba nan take ba.
"Kaitsaye ta wuce receptionist ta yi magana da ba za ta wuce ta 60 seconds da wanda yake kula da dakunan hotel din.
Sannan ta nufi upstairs ba ta yi wata doguwar tafiya ba ta iso wani dogon corridor, rooms ne birjik.....suna facing juna ahankali take duba d'an k'aramin allo da ke dauke da rooms numbers, har ta yi nasarar gani room 402 hankali kwance ta yi knocking, wani mutum mai matsakanci tsawo fuskarshi lullu6e da face masks kwayar idanuwanshi kawai ka ke iya hangowa ya bude mata k'ofa ta shiga d'akin.

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:50 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*9*

Rigar jikinta ta fara cirewa ta jefa bisa gado, ta nemi gefen gadon ta zauna yayin da Jarumi ke safawa da marwa daga farkon bangon gabas zuwa bangon yamma, ya nad'e hannaye a bayanshi.
"Zai kyau ka nemi wuri ka zauna mu yi magana da ke gabanmu.
Cewar Momma tana nuna masa kusa da ita da d'an yatsanta.
Cikin kaukkausar muryarsa mai cike da ban tsoro ya ce ba zan zauna ba Zaituna har sai kin fad'a min ta ya ki ka yi sakaci har asiri da ke jikin Muhammad ya karye, har yake da gwari gwiwar nemowa Aliyu aure?"
"Karka yi min wannan tambayar banza Jarumi saboda banida amsarta, kawai ka nemo mafita ba wai ka tsaya kana dawo da hannun agogo baya ba.
Kukan kura ya yi ya chafke mak'oshinta, ya shek'eta kamar zai rabata da ranta tsananin azaba yasa momma kwantawa ya bi ta ya haye ruwan cikinta, sai da ya ga ta kusa daina motsi sannan yasake ta ya sauka daga kanta.
Yayin da tari ya turnuk'e ta, da kyar ta iya tashi zaune robar ruwan Faro ya dauko a fridge ya jefa mata.
Jikinta na rawa ta balle murfi ta kafa baki tasha rabin ruwan duk ya zube mata a jiki.
Cikin angry Voice ya ce ki shiga taitayinki da ni kinsani sarai banida mutunci, bana d'aya daga cikin mutane da ke jure rainin hankalin tsohuwar kilaki irinki, don haka ki natsu ki saurari irin hasara da ki ka janyo mana.
Ajiyar zuciya mai k'arfin gaske momma tayi, had'e da shafar wuyanta da ke ji tamkar an daure mata shi da igiya, yayin da idanuwanta sun kad'a sun yi jajir.
Afusace Jarumi ya cigaba da cewa duk wurin malamin da na je magana d'aya ce, tabbas sai Aliyu ya yi aure don haka ba mu da za6i illa mu kashe yarinyar bayan aure.
Sai abu na gaba muddin kina so hakkar mu ta cima ruwa, dole sai kin hana Aliyu kusantar yarinyanan malam ya gayamin muddin suka yi tarayya, komai na mu ya rushe duk wani wahala na tsawon shekaru 28 ya rushe.
Hannunshi yasaka a pocket d'in rigar shaddar da ke jikinshi, ya ciro wasu bak'ak'en layu ko kallonsu ka yi sai gabanka ya fad'i ya mik'awa Momma, ki binne su dai-dai wurin da ki ka san Aliyu zai taka.
Hannunta na rawa ta kar6a ta shiga jujjuya su.
Sake dauko wata batta ya yi wacce aka lullu6e da fatar damisa, wannan kuma ki turare shi idan ki ka san Aliyu zai shak'i k'amshinsa karki sake wani ya ji k'amshinsa fa ce Aliyu, kinji ko?"
Gyad'a kai ta yi kafin ta gyara zama muryarta bata fita wtsosai saboda shak'ar da ya yi mata, ta ce ba ka yi min gamsasshe bayani magani na menene?"
"Shiru ya yi kamar ba zai yi magana ba daga bisani ya zauna kusa da ita, ya dafa kafad'arta

ya yi kasa da murya tamkar mai rad'a ya ce amfanin wannan magani shine mazakuta Aliyu zai mutum mutusss, koda tsirara ya ga mace ba zai ji sha'awarta ba.
Karki manta sihiri da ke jikinsa na tsanar aure ne da tsanar mata ba na sha'awarsu ba, ki sani kasancewar Aliyu da wannan yarinya a waje d'aya dole wata rana zai ji sha'awarta, idan har ya had'a shinfid'a da ita daga ni har ke kashinmu ya bushe don haka ki kiyayye.
"Shikenan idan wannan ne Jarumi bakada matsala.
Da kyau 'yar gari sai ki tashi ki tafi, na gama magana Sai dai idan wani emergency ya taso zai nemi ki.
Mik'ewa tayi tasaka rigarta da black shade d'inta, ta kuma zuba guzirin shed'an d'in da yabata a handbag.
***---****----****

Da misali k'arfe 5 na yammaci Aliyu yana zaune a office d'inshi, ya duk'ufa akan system dinshi aiki yake sosai.
Aka yi knocking k'ofa yes!
Yafad'a batare da ya kalli me shigowa ba,
Sakatariyarshi ce Ester.
Cikin girmamawa ta ce Sir Jamal ne ya zo kasan da zuwanshi a shigo da shi.
"Sai a lokaci ya d'ago darara idanuwanshi, masu masifar tafiya da imani 'ya mace ya ce ki shigo da shi mana.
Okay sir!
Tafad'a had'e da juyawa.
Bata jima da fita ba Jamal ya shigo hannu ya mik'awa Aliyu suka yi musabaha kafin ya ja kujera ya zauna, ya ake ciki abokina tun jiya yakamata mu tatttauna zance barrister sai dai rashin wadattace lokaci ya hana mu?"
"K'ayattace murmushi Aliyu ya yi ya mayarda laptop dinshi gefe, ya kalli Jamal a natse ya ce gaskiya ba laifi Barrister tana da kyau sosai kuma da alamu tana da kyau hali, sai dai banji sonta ko k'ank'ani ya shiga zuciyata ba, kawai dai yanayin shigarta da yadda take magana ya burge ni, matuk'a.
Amma a haka zan daure na aureta tunda an riga an mak'alk'alamin ita bani da za6i.
"Jamal ya yi murmushi tare da jinjina zance abokin nashi, ya gyara zamanshi yana duban Aliyu cikin sanyaya murya ya ce ina gani tunda har ka amince wannan ba abin damuwa bane duba da biyayya ce za ka yi ma mahaifinka,
"Inaso ka dauki zance da muhimmanci kada kayi halin ko oho da lamarin barrister, ba mamaki ita ma biyayya ce za ta yiwa nata iyayyen ina rok'o ka abokina da kayi abinda ya kamata.
"Ta6e baki Aliyu ya yi yana yatsine fuska "to ni miye nawa aciki?"
Daddy ya ce in shirya naje naga yarinyar na kuma je, bayan nadawo na shaida mishi ta yi sai dai gaskiya ban nuna mishi bana sonta ba, yanzu dai lokaci biki kawai nake jira.
"Ba damuwa abokina idan da rai da lafiya two months kamar gobe ne, yanzu yaushe za mu sake komawa wajenta?'
"Banaso a sami matsala daga gareka.
Cewar Jamal yana duban Aliyu.
"Gaskiya yanzu bani da lokaci akwai d'inbin ayyuka agabana, kuma ma miye amfanin zarya gun

yarinyar da banida ra'ayinta, ina ce sai in kana son mace ka ke d'oki da rawar jiki son ganinta?"
"Gaskiya hakan bai dace ba abokina kadai duba, koda zuwa end of this month ne mu kai mata ziyara wallahi yarinyar tana da kirki matuk'a.
"Shikenan Jamal zan duba nagani amma a halin da ake ciki yanzu bani da lokaci, sai mu jira zuwa k'arshen wannan watan.
Ba damuwa abokina kadai k'ok'arta.
Dariya Aliyu ya yi a takaice ya ce naga alama kai da barrister ta ku ta zo d'aya.
Dariya Jamal ya yi yana mai mik'a masa hannu suka kashe.
***----***---****
*YOLA*

Barrister Amina  tare da Barrister Zarah suka jero suna fitowa daga magistrate court 3.
Barrister Zarah ta dubi barrister Amina ta ce bebs ya had'uwarku da Aliyu ta kasance hope guy ya yi miki?"
"Murmushi Barrister Amina tayi tace Ba laifi ya amsa sunanshi namiji yana da kyau sosai da cikar kwarjini, ya had'u irin had'uwar da kowace 'ya mace take buk'ata.
Ya yi miki kenan?"
Ba laifi gaskiya karo na farko a rayuwata da naci karo da namijin da naji farat d'aya ya kwanta min a rai.
Ta k'asara magana tana tunowa da fuskar Aliyu.
masha Allah!
Haka nakeso ji daga gareki bebs fatana Allah ya had'a kawunanku ya kade duk wata fitina da ke ciki.
Amin! Bebs.
****----****-----****
A kwana atashi asarar mai rai yau gashi saura sati uku  bikin Aliyu da barrister Amina, zuwa wannan lokaci abubuwa da dama sun faru daga ciki akwai masu dad'i akwai akasin hakan.
"Kud'ad'e masu kauri gaske Daddy ware ya ba k'anwarshi Salma ta je Dubai ta had'owa Aliyu kayan lefe na gani na fad'a taci mutuncin naira ba kad'an ba.
Daddy bai saka momma cikin hidimomin bikin ba, asalima ma bata san da zance lefe ba, sakamakon yadda ya ga tana nuna adawarta akan aure a fili, tun abin yana bashi mamaki har yadawo bashi tsoro lokaci da ya sanarda Salma zance ita ce ta bashi shawarar ya dinga 6oye Mata duk wani abinda ya yashafi zance auren na Aliyu, har zuwa lokaci da za'a yi biki saboda basu san miye manufarta ba.
nan take Daddy ya yi na'am da shawarar Salma saboda shi kanshi lamarin na masifar daure mishi kai.
"Akwati goma sha biyu Salma ta had'a har da tsaddadiyar mota akai kirar cadillac, lokaci da aka kai lefen gidan Barkido ya yi fad'a sosai a cewarshi bayason bidi'a da kyar dangi suka shawo kanshi ya amince aka kar6i kayan.
"Barrister Amina kwance akan gadonta ta yi zurfi a tunanin Aliyu abu d'aya ya ke daura mata kai, ya kuma jefa zuciyarta cikin tunani shi ne tunda Aliyu ya zo sau d'aya bata k'ara jin d'uriyarshi ba.
Sai kayan lefe aka kawo gidansu shin me hakan yake nufi?"

Anya kuwa Aliyu yana sonta?"
Wad'annan su ne tambayoyin da tarasa wanda zai bata amsar su.
"Mtsss....!
Ta ja tsaki ta dauki pillow ta matse gam a k'irjinta, ta d'an girgiza kanta cike da haushin kanta ta tuna da halin da ta tsince kanta, game da Aliyu domin tun daga ranar da idanuwanta suka ganshi, sai tunaninta ya canza zuciyarta ta bijiro mata da wani al'amari mai wuyar fassarawa.
Tsundun ta tsunduma begen Aliyu al'hali shi d'in bai san tana yi ba.
Ba ko shakka tasan ta kamu da soyayyarshi mai zafin gaske, duk da tana da labarin bai cika zama wurin d'aya ba, shi mutum ne mai yawan tafiye-tafiye ak'alla ace yana kiranta a waya ko gaisawa su yi koda bai mata firar soyayya ba.
Yaushe ma ya ga numbernki da zai kira ki.
Wani bangare na zuciyata ya ce da ita.
Yanzu ahaka za su yi aure al'hali bai da lokacinta, kenan hakan za su yi zaman aure?"
A karo na biyu tasake jan tsaki mtsss!
Cike da takaici zuciyarta sai rad'ad'i take mata, sosai take ji zafin kanta yadda ta shiga damuwa akan mutume da bai ma san tana yi ba, asanyaye ta mik'e tashiga bathroom sakamako kiran sallar magarib da aka fara.
***----****----*****
*LAGOS*

Aliyu na zaune a office dinshi da ke Lagos ayyuka sun masa yawa ba kad'an ba, duk da yau ya sami sassaucin aiki, a matukar gajiye ya jingina bayanshi ga jikin kujera da yake zaune akai a hankali ya zare sun shade glass din da ke manne a kwayar idonshi, tare da lumsashe idanuwanshi wayarshi tayi ringing har ta tsinke bai d'aga ba, a karo na biyu tasake ringing sai da ta kusan tsinkewa ya mik'a hannu ya dauka batare ya bud'e idanuwanshi ba ya yi picking ya kara a kunnenshi.
"He...llo!
Yafad'a chan k'asan mak'oshi.
ka ci gidanku Sultan.
Ba shiri Aliyu ya ware idanuwanshi ya kuma gyara zamanshi, sakamakon muryar Daddy da taki dodon kunnenshi.
"Dad ina wuni?"
Ban san inda yake ba.
Cikin shagwa6a Aliyu ya turo baki yana cewa Daddy....am sorry!
Duk da ban san laifi da nayi ba.
Fad'a sosai Daddy ya shiga yi mishi ta hanyar cewa karka maidani mutume banza Gadanga, sau nawa ka je Yola wurin Amina bayan zuwanka na farko?"
"Tsuke fuska ya yi kamar Daddy yana ganinshi, ya ce Daddy am too busy ban samu zuwa ba ayyuka ne suka yi min yawa.

[7/26, 11:50 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*10*

Amma duk lokaci da na samu sassaucin aiki zan shirya in je, amma kuma Daddy sai nake gani ko ban je ba zan iya aika P.A na kamal amadadi na, sai ta yi mishi list na abunda take buk'ata ko nawa ne zan ba t.....
"To hell with you ka da kud'in naka Gadanga.
Daddy ya katse cikin fushi Daddy ya cigaba da cewa an gayamaka komai ne kud'i suke iya siye, in fact yarinyarnan ba 'yar matsiyata ba ce ita kanta mai kud'i ce balle aje ga iyayyenta.
Yadda ka ke tink'aho ubanka mai arziki ne ita ma nata uba mai arziki ne, inaso ka jingine zance kud'i a gefen ka natsu kasan me ka ke yi, saboda kai ba k'aramin yaro bane.
"Aliyu kamar zai fashe da kuka yake shafa sumar kanshi kafin ya ce kayi hak'uri Daddy I don't mean to hurt you am just try to tell you how busy I'm but am so sorry, zan yi k'ok'ari gobe na biyo morning flight nayi weekend a Yola.
"That's my favourite boy haka nakeso ji Gadangana.
kafin Daddy yasake magana ya katse kiran had'e da jefa wayar bisa file d'in da ke gabanshi, ya tsurawa wayar ido yana girgiza k'afarshi, zazzafar ajiyar zuciya ya yi had'e da jin haushin Daddy

ganin da k'arfi da yaji yana so ya mak'alk'ala masa auren yarinyar da baya jin sonta a zuciyarshi.
"Zuwa wannan lokaci yaci ace Daddy ya jinjina masa da namijin k'ok'arin da ya yi na amincewa da auren, yaci ace ya yaba masa ya kyale shi yaji da k'unci da rad'ad'in da zuciyarshi take mishi, ya Daddy yakeso ya yi da rayuwarshi ne?
"Shi mutum ne da bayaso damuwa ko kad'an sai gashi stress yana so ya yi mishi yawa.
ya jima shiru yana nazarin abinda ya kamata ya yi, yasan tabbas bashi da mafita dole yaje Yola, musanmman yadda ya daure kanshi har da wani cewa zai yi weekend a can, ya zame mishi wajibi dole ya je ko baya so in dai yana so zaman lafiya tsakaninshi da Daddy.
Ya d'ago kan ya dubi wrist watch d'in hannunshi sannan ya mik'e tsaye ya dauki wayoyinshi ya bar office duk da yana da tarin ayyuka masu matukar muhimmanci.
****----****----****
*ABUJA*

Momma tafito daga apartment d'inta jikinta sanya da buba ta material black & golden colour, kaitsaye apartment d'in eMaryam ta nufa dai-dai k'ofar shiga main parlor ta tararda wata 'yar kyarmusasshiyar mata tana jiranta, barka da fitowa Hajiya!
Yauwa Ruky!
Shigo daga ciki ki ganta kwananan jikinta ya fara sauki sosai, momma tafad'a tana wucewa gaba Ruky na biye da ita tun daga main parlor za ka fara ji gurnaninta, tsaki momma ta ja mtsss!
wata k'ofa ta nufa ta sanya key ta bud'e wani irin masifafe wari ya bugi hancinta babu shiri ta doshe hanci da tafin hannunta, cikin fushi ta shiga kwalawa inna Laraba kira inna laraba.....inna laraba fa!
Da gudu tafito daga bedroom d'inta d'an kwalinta a hannu, cikin yanayi na tsoro ta k'araso gani Hajiya.
Wannan wane irin wari ne ke fitowa daga d'akinan?"
Jikin inna laraba yana rawa ta shiga d'akin, Maryam na takure a jikin bango sai fizgar gashin kanta take tana wani irin gurnani bakinta na fitarda miyau mai yauk'i, k'afafunta da hannayenta daure da sark'a abin gwanin ban tausayi.
Cikin rashin tsoro Inna laraba tanufi wajenta, tashiga dubata tagano kashi ne tayi d'agata tayi tanufi bathroom da ita ta tsaftattace mata jiki had'e da sauya mata kaya ta fito da ita bisa gado ta zaunarda ita, ta dauki tissue ta goge inda kashin ya6ata tayi mopping ta kuma fesa air freshner sannan fa momma da Ruky suka shigo duk da haka sai wani yayatsine fuska momma take.
"Cikin daure fuska momma ta dubi inna Laraba ta ce inna ba mu wuri likita za ta duba ta.
To!
Cewar inna Laraba tana mai ficewa daga d'akin.
Daf da Maryam momma ta tsaya ta d'ago ha6arta cikin zallan rashin imani ta dauke ta da mari, sai da ta kai kwace, sai kawai ta rufeta da duka tana yi tana zurfa mata zagi shegiya tsinaniya muddin ina raye kin dinga gani bala'i da masifa har karshen rayuwarki.
Ba dai kin k'i mutu ba tsawon shekara ashiri da takwas ina azabtarda ke, da yake ran kare ne da ke kin k'i mutu ki hutarda kanki nima in huta, to tunda kin kafe mu zuba ni da ke d'a halak ka

fasa, shegiya mai taurin ran tsiya.
Ta k'arasa magana tana huci.
Dafa kafad'arta Ruky tayi cikin sigar rarrashi ta ce don't worry Hajiya komai yana da lokaci tunda ki ka iya jure zama da ita na tsawo shekaru 28 kisanta ba zai miki wahala ba.
"Bana so na kasheta ne da kaina Ruky na fi so wahala ta kashe, ta kinga ba wanda zai zargeni.
"Haka ne Hajiya you're too smart.
Dariya momma tayi cike da jin dad'i an ya6e ta.
Yi maza Ruky ki yi mata allurar haka kawai 'yan kwanaki nan da aka daina yi mata allura tafara acting like normal mutane, kin ko ga ba abu mai sauki bane na barta ta wark'e don haka daga yau kin dinga yi mata allura kenan.
"Murmushin mugunta Ruky tayi ta bud'e handbag tafito da wani Vaccination, saida ta cika sirinji ta kama hannu Maryam wacce tun lokaci da momma ta jingeta take kwance lamo kamar mai bacci, ga jijiyar hannu Ruky tai mata allura ko motsawa bata yi ba cikin abinda bai wuce 30 seconds ba tayi bacci.
"Wani mushirikin murmushi momma tayi tana k'arewa Maryam kallo, sannan ta juyo ta nufi k'ofar fita yayin da Ruky ta mara mata baya flat d'inta suka nufa.
"A main parlor suka tarar da Tima zaune tana wasa da yatsun hannunta, kamar mai lissafi momma ta dube ta ta ce Tima me ki ke yi anan?
Ba na hanaki zama a falonan ke kadai ba, ina zee-zee da Minat da suka barki ke kadai?"
Har momma ta gama zuba mata tambayoyi bata kalleta ba, sai wasanta take da yatsunta.
"Tima.....magana nake da ke fa.
Wani irin d'agowa tayi idanuwanta sun yi jajir sai kace abinda aka zubawa Barkono, ta mik'e zubur ta nufi wajen momma da sauri momma ta ja da baya cikin wata rikitattaciyar murya ta ce "za ta zo tabbas tana gam da zuwa ita ce za ta tone rijiya mai dauke da macizai da kunamu ta fito da jar jakka mai dauke da kundin sirri.
Tana gama magana ta juya ta nufi d'akinta tai barking k'ofar da k'arfi gaske.
momma da Ruky suka bi ta da kallo, girgiza kai momma tayi cikin rashin daukar Maganar Tima da muhimmanci ta nufi sofa ta zauna wacce ke kallonta ta nunawa Ruky ta zauna.
Hajiya ina tausayi Tima wallahi, har nake gani kamar zunubin da ki ka aikata ne yake bibiyarta.
Murtuk'e fuska momma ta yi kamar bata ta6a dariya ba, hakan yasa Ruky ta sha jini jikinta.
"Duk haka sai da momma ta nuna mata k'ofar fita da d'an yatsanta, tashi maza Ruky ki fice min daga gida aiki ki ke min kuma ina biyanki mak'udan kudi bana wasa ba, daga yau sai yau ina gargadinki kar ki sake yi min kutse a cikin al'amurana duk duniya bani da babban mak'iyi irin mai fad'amin gaskiya.
"Allah ya ba ki hak'uri Hajiya na tu.......
Ya isa dallah kin riga da kin batan rai ki fita kawai sai gobe in kin zo.
Mik'ewa Ruky tayi sahunta a likkafa ta fice cike da takaici irin wulak'ancin da momma tayi mata.
****___****____****
*YOLA*
Misali k'arfe goma sha biyu na rana jirgin da Aliyu ya shigo ya yi landing, direbansu na yola ya kira ya dauko shi daga Airport gidansu da ke nan Yola ya sauka ya yi wanka ya shirya masjid ya fara wucewa ya yi sallar Juma'a daga masallaci, ya wuce gidan uncle suraj anan ya ci abinci

suka shiga tattauna zance business duk lokaci da uncle Suraj ya dauko zance aurenshi sai ya shasshata zance.
Anan ya yi sallar la'asar, kafin ya yi sallama da uncle ya nufo gidansu Barrister Amina.
"Barrister Amina ta kammalla shirinta tsaf cikin Arabian gown ash colour tayi rolling da d'an siriri veil orange colour, ta fito sak'ale da handbag d'inta ita ma kalar orange tayi masifar kyau da yake Ummi ta fita shiyasa ta lek'a d'akin mai aikinsu Asabe ta ce koda Ummi ta rigani dawowa ki fad'a mata na fita saloon gyara gashi, gudu-gudu ta fito saboda daga wurin saloon tana so ta biya gidan Barrister Zarah Ladan tun kafin ta k'arasa parking lot tai using remote k'ofufin motarta suka bude ta shiga tayi ma motar key tayi reverse, ta nufi gate sai gate d'in a bude wata dalleliyar mota kirar Jeep Volkswagen, ta shigo dole tai reverse ta koma baya ta bata wuri ta wuce a tunaninta ko d'aya daga cikin guest d'in Abba ne, wani abin takaici ba kowa a gida dole ta tsaya tai entertained d'insu, ta kashe motar had'e da jan tsaki mtssss!
Ta bude k'ofa ta fito yayin da bak'in suka yi parking, direba ne yafara fitowa ya bud'ewa Aliyu k'ofa ya fito tai tsaye turuss....tabbas ta shaida fuskar Aliyu cikin salon tafiyarta mai daukar hankali ta isa wurinshi, fuskarta dauke da sanyayye murmushi sannu da zuwa!
Ta fad'a kamar mai koyon magana.
Cikin husky voice dinshi ya ce Yauwa mun same ku lafiya?"
Lafiya qalau ya su mommy?"
Lafiya qalau suke.
masha Allah!
juyawa tayi wajen gate man ta yafuto shi da hannu, cikin azama ya iso ta ce ka shiga da bak'o falon bak'i ina zuwa tak'arasa magana had'e da nufar cikin gida.

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:52 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*11*

Ta kwalawa Asabe kira ta tayata had'a mishi abinci da drinks, ta dubi Asabe ta ce dauki ki kai masa Asabe ki ce mishi ina zuwa.
"Bayan Asabe ta kai mishi abinci ta dawo ta lek'a d'akinta ta ce ta kai mishi saida iya juice ya sha ya ce ya k'oshi da abinci, shikenan Asabe ki mayarda abincin kitchen.
Ta mik'e ta isa gaba dressing mirror ta gyara fuskarta, ta fesa Asrar alhub perfume sannan ta fice cikin sanyayar muryarta tayi sallama ya amsa can k'asan mak'oshi, sai da ta zauna a sofa da ke facing nashi sannan tasake gaidashi ya amsa a tsanake, shiru ya biyo baya kowanesu da abinda yake sakawa a ranshi wayarshi tayi ringing hakan yasa ta d'ago ta sace kallonshi ya yi receiving call d'in cikin tsadadd'en turancinshi yake magana, da business partner dinshi tsawo 30 minutes ya dauka yana waya kafin ya katse kiran ya d'an sace kallonta dai-dai ita ma ta d'ago ta kalleshi karaf idanuwansu suka sark'e, wani irin kwarjini na musanmman kwayar idanunshi tayi mata fiyye da farkon ganinta da shi, kamar daga sama taga yasake mata k'ayatattace murmushi wani irin sanyi ya ratsa tun daga tsakiyar brain d'inta har zuwa tafin k'afarta.
"Ita kanta batasan lokaci da ta mayar masa da martani murmushin na shi ba.

"Cikin salon maganarshi mai cike da yanga da aji ya ce Barrister da fatan za'ayi min afuwa kasancewar kin gani daga sama ba sanarwa, wannan ya faru ne a dalilin rashin sanin phone number dinki kiyi hak'uri da rashin ganina ayyuka ne suka sha min kai, yanzu dai bani digit dinki gudu kar a koma 'yar gidan jiya.
Yakarasa magana yana shafar geminshi.
Ta sadda kanta K'asa fuskarta dauke da yalwattace murmushi, ta shiga karanto masa numbers dinta duka guda biyu da ta ke using da su.

"Ya shigar da digit din a wayarshi ya yi saving da Barrister 1 da kuma barrister 2 ya kira numbers da wayoyinshi a lokaci d'aya phones d'inta guda biyu babban da k'arama suka yi ringing ta kai dubanta ga wayoyi ni ne kiyi saving numbers d'in yafada kamar mai koyo magana.
"murmushi kawai tayi batare da tayi magana ba, haka Kuma bata kalleshi ba.
Shiru ya biyo baya na tsawo wasu dak'ik'u, gani za su 6ata lokaci a banza shi kuma ba abinda yafi ba muhimmanci irin lokacinshi saboda kowace dak'ik'a tana da matukar amfani a wurinshi,

a cewarshi idan lokaci yawuce shikenan ba zai ta6a dawowa ba shiyasa yake matuk'ar mutunta lokaci.

"Don haka ya gyara zama duk da shi d'in ba gwani surutu bane, amma kuma ya zama dole ya yi shi a gaban barrister sakamakon fahimtar da ya yi ita ma gwanace a fagge miskilanci, sosai yake mamaki yadda zamansu zai kayya shi da ita.

Ya yi gyaran murya kamar mai shirin kiran salla, ya ce Barrister maganarki tsada ne da ita ko ya ke ki ke presented case a court oho!"

Yadda ya k'arasa magana yana rik'e habbarshi yai masifar bata dariya, har batasan lokaci da tasaki dariya mai k'aramin sauti ba har tana had'awa da rufe fuska da tafin hannunta.

"Shi din ma murmushi ya yi ya cigaba da cewa kodai har yanzu fushi ake da rashin zuwa na.

"Girgiza kanta tayi ta kalle shi da raguwar murmushi a fuskarta ta ce "A'a Allah ni ba fushi nake ba duk abinda ka fad'a ina saurare kuma na fahimci bayaninka.

"To amma ai ba ki ce da ni komai ba duk da hak'uri da na bayar anyya kuwa barrister kin hak'ura kodai na nemo paper da biro na rubuta miki I'm sorry ma'am sau dubu?"

"Zaro golden eye's d'inta ta yi had'e da furta rufa min asiri yalla6ai, ni asuwa da zan ba ka wannan danye aiki.

Ke barrister mana masu murd'e gaskiya ta koma k'arya ku murd'e k'arya ta koma gaskiya.

"Turo baki tayi cikin shagwa6a da ita kanta batasan tayi ba, abinka da sangartattaciya ta ce ni gaskiya ba haka nake ba ka je ka bincika sosai za'a gayamaka bana d'aya daga cikin masu aikata wannan aiki saidai in kuma akasi aka samu, wannan kam ba zan maka musu ba saboda d'an adam azaji ne.

"D'an ta6e baki ya yi ya d'age girar ido yana kallonta wanda hakan ba k'aramin masifar k'ara masa kyau ya yi ba, ya ce gashinan yanzu ina ba ki hak'uri kin k'i hak'ura.

"Ta d'ago ta dube shi da yalwatattacen murmushinta har sai da dimple d'inta duka biyu suka lotsa, hakan yasa kyawun fuskarta ya k'aru cikin sanyinta had'e da tattausan lafazi ta ce "Don Allah yalla6ai ka rufa min asiri kuma ai zance bani hak'uri bai ma taso ba saboda ba wani laifi da aka yi min ba.

"Murmushi ya yi ya ce shikenan tunda kin ce haka.

Daga haka ya yi shiru dama can ya gaji da surutu saboda har kanshi fara ciwo, shi kanshi yana mamaki yadda ya barke baki yana zuba a gabanta.

"Gani yadda ya yi shiru ta gano fuel dinshi ya k'are saboda haka ta gyara zamanta, tana wasa da bangles d'in hannunta ta ce yau ina ka baro Jamal?"

"Saida ya dauki lokaci kafin ya ce "lafiya qalau yake munyi waya da shi kafin na iso nan da yake daga Lagos nake kaitsaye daga can nayo nan, shiyasa ba ki gan mu tare ba.

"Ayya!

Ta fad'a tana murmushi.

Sai kinyi hak'uri da ni Barrister saboda yana yin aikina ban cika zama ba sosai yanzu haka on Monday zan tafi business trip a Zurich sai satin bikinmu zan dawo don haka duk abinda ki ke buk'ata Jamal ko kamal P.A na za su kawo miki, amma zaki rik'a jin wayata duk lokaci da na samu sarari.

"Ba dawuwa Allah ya taimaka!

"Amin ya fad'a yana mik'ewa tsaye zan wuce sai gobe in na shigo, ki gaida mommy in sun dawo.
"Ita ma mik'ewa tayi had'e da cewa zasu ji an gode kwarai Allah ya tsare.
Ya gyad'a kai had'e da ficewa da sauri shiyasa bata sami damar raka sa ba ta koma cikin gida, ko zama bata yi ba maigadi ya dinga shigowa da manya-manya shopping bags yana ajiye had'e da wasu manyan kwalaye.
Ya kuma mik'a mata envelope mai dauke da kud'ad'e masu yawan gaske, ita kanta sai da ta jinjina yawan kud'in.
"Ta zuge zip d'in handbag d'inta ta jefa envelope d'in ta kira Asabe ta shigarda kayan store.
Ta dauke jakkarta ta sake fitowa ta ja motarta ta nufi wajen saloon.
****""*****""****
*WASHE GARI*

Barrister A da kanta ta shiga kitchen ta had'a mishi had'add'u dishes, sai misali k'arfe 4:20pm ya iso lokaci da sak'on isowarshi ya riske ta tana zaune ta shirya cikin red colour din straight rubber gown mai adon stones a jiki tai masifar fitowa da shape d'inta, ta yane kanta da scarf multi colour jikinta na fitarda k'amshi Dima da Asrar ahub perfumes.
"To na ba ka umarni sai ka ja motar mu tafi, kana k'ara 6ata mana lokaci.
A tunaninta idan ya gama magana da Isah zai kulata sai taga sa6ani hakan.

Don haka ita ma taja bakinta ta tsuke Bata k'ara cewa uffan ba har sanda suka iso hall d'in, suna fitowa ya rik'o hannunta suka k'arasa ciki hall, dinner ta k'ayatarda Aliyu matuk'a a cewar shi duk events d'in suka yi ba wanda ya burge shi irin dinner d'in, saboda ba hayaniya sai slow music ke tashi anci ansha anyi couples dance sai kusan 1:00am aka tashi kowa ya kama gabanshi.

"Tun a mota tafara bacci har suka iso gida bata saniba, tasheta Aliyu ya yi ta hanyar cewa barrister ki tashi mun iso gida.
ko motsawa bata yi ba ji ya yi zai iya tafiya yabarta anan, har ya bud'e mota ya fita ko me ya tuna sai dawo gefen da take, ya shiga bubbuga hannunta da k'arfi bugu d'aya zuwa na biyu ta bud'e idanunta masu cike da bacci.
"Fahimta abinda ke faruwa tayi shiyasa bata furta uffan ba tafito tana rangaji tana had'a hanya ta nufi cikin gida, dai-dai k'ofar shiga main parlour ta kusa fad'uwa da sauri ya tarota ya rik'o shoulder ta, ya d'an rungume rabin jikinta yayin da ya sak'ala d'ayan hannunshi akan waist d'inta.
"Wani irin kunya taji ya lullu6eta sakamakon yadda ya rungume waist d'inta nan take ta wartsake daga baccinta, a haka suka cigaba da tafiya har zuwa bedroom d'inta.
A gefen gado ya zaunar da ita ya kalleta ta k'asan ido ya ga yadda take lumshe ido alamar bacci bai gama sakinta ba, ya ce kiyi k'ok'ari ki rage kayan jikinki za ki fi jin dad'i kwanciya.
Daga haka ya juya har ya murde handle ya d'an juyo cikin wani irin murya ya furta "Good night!
Murmushi tayi kafin ahankali ta ce "Good night!
Haka kawai ta tsince kanta cikin nishad'i marar misaltuwa, umarninshi tabi ta hanyar sauya kaya zuwa sleeping dress.
****""***""""*****
Washe gari!

Kasancewar gajiya tayi musu yawa hakan ya basu damar yin bacci, Kuma da yake daga gidan Daddy ake kawo musu abinci.
"A kwana na shidda da bikinsu tana zaune a falonta tana tunani fara girki a yau, saidai batasan miye favorite d'inshi ba.

Gani za ta wahalada kanta a banza yasa ta mik'e ta nufi falonshi da ke upstairs, ta tura k'ofar ta shiga da sallama zaune ta sameshi yana aiki a system.
Jin motsi bud'e k'ofa da kuma k'amshi fitinane turareta ya bugi hancinshi, yasa d'ago da kansa ya kalleta sai kuma kauda kai ya cigaba da aikinshi.
Cikin tattausan lafazi ta ce barka da hutawa Yalla6ai!

Saida ya6ata almost 20 seconds kafin ya amsa da yauwa ya akayi ne?"

Yalla6ai dama zuwa nayi na sanarda kai yau inaso nafara girki da kaina, saidai bansan abinda ka fi so ba.
"Uhm!
Ke nan kin iya girki ne?"
Bata yi mamaki tambayarshi ba saboda tasan fiye da hakan ma, zai iya aikatawa.
"Ba laifi ina k'ok'artawa.
Uhm!
Ba ki iya ba kenan?"
Sai an bani dama anan za'a gane iyawa na.
Ki yi hak'uri da girki nan har mu je Abuja, tsananin dad'ewarmu a garinan ba zai wuce 7 days ba.
Shikenan tunda haka ka za6a na barka lafiya, takarasa magana had'e da ficewa.
Bayanta ya bi da kallo kafin dawo da ganinshi akan system.
Haka zamansu ya cigaba da kasancewa kowa yana sha'anin gabanshi, tun abin yana damunta har ta zo tafara sabawa dama tasan baya sonta, bata tunani zai so ta koda zuwa gaba ne.
Shiyasa tayi hak'uri da yadda ta tsince kanta aciki, ko ba komai ta fitarda iyayyeta kunya, ta kuma yi musu biyayya dama kuma ance bin na gaba bin Allah.

***'''***'''***'''***

Da misali k'arfe 5:00pm na yammacin ranar tana zaune a falonta, Indian series take kallo, text ya shigo wayarta a zatonta ko alert ne.

Saboda tana expected d'in wasu kud'ad'e da azama ta dauki wayarta, ta shiga inbox *ki shirya za mu je ki yiwa su momma bankwana tomorrow morning za su wuce Abj ki shirya yanzu nan karki 6atamin lokaci*
Murmushi tayi had'e da girgiza kanta ganin yanzu nan ya wuce ta, amma tsabar ya tsaneta ba zai iya yi mata magana ba shine yake turo mata text.
"Ta tashi jiki asanyaye tashiga bedroom d'inta ta canza kaya zuwa wata French gown, maroon colour tayi rolling da white scarf, tasaka takalmi heel tafito rik'e da 'yar k'aramar purse d'inta a hannu sai zuba k'amshi take.

Jeeddah Aliyu
[7/26, 11:59 PM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*19*

A main parlour ta tararda shi tsaye yana jiranta, yana sanye da fari material na maza wanda ya yi masifar k'ara fitowa da kyakyawar halittarshi, tana fitowa yafice zuwa parking lot.
Tabi bayanshi tuni Isah direba ya jawo mota, ya fito ya bud'e musu k'ofa suka shiga yaja motar suka fice daga gidan.

K'amshin perfume d'inshi ya garwaye da nata ga kuma sanyi Ac motar, ya had'e ya bada wani daddad'an k'amshi mai tafiyar da ruhi da gangar jiki.

"Tafiyar kurame ce ake yi daga shi har ita ba wanda ya furta uffan, afakace ya sace kallonta ya dauke fuska.
Gani ba girmanshi bane satar kallonta yasa ya fito da wayarshi ya kira wani business partner d'inshi.
"Hakan yasa ta mayarda hankalinta ga kallon gefen titi.

Koda suka iso gidan ya wuce gaba ta bi shi abaya har zuwa sitting room d'in gidan, anan suka iske momma zaune da alamar tasan da zuwan nasu.
Barrister A ta durk'usa har k'asa gwiwa biyu-biyu ta gaidata.
"momma wacce ke hakince akan two sitter tana shan k'amshi wanda atsawon rayuwarta ba'a ta6a gaidata haka ba.
"Kauda fuska tayi tana wani yatsina, ta bud'e baki da kyar ta amsa da kina lafiya?"
"Lafiya qalau!

Cewar barrister A da yake ita ba k'aramar yarinya bace, ta hango tsan-tsan kiyayyarta a kwayar idon momma.

Shi kanshi Aliyu bai ji dad'i yadda momma tayi mata ba, shine ya yi k'arfin hali cewa tashi ki zauna akan kujera.
"Girgiza kai tayi ta gyara zamanta akan rugs carpet ta sadda kai k'asa, girls d'in momma na shigowa falon suka yi arba da ita suka sa ihu, har rige-rige zuwa wurinta suke.
"Hatta Teema da batada lafiya dariya take tana tafa hannayeta, tana jujjaya kanta alamar tana farin ciki ganinta.

"Sai lokaci ta d'an saki jikinta, tana murmushin yak'e, hannunta Teema ta k'ank'ame sai faman lek'e fuskarta take tana dariya.
"Sosai haushi ya turnuk'e momma gani yadda girls d'inta suke tarairayarta, tsawa ta daka musu kai miye haka?"
Dallah ku ja Teema ku koma d'aki.
Kuka Teema tasa tana bubbaga k'afa a k'asa tana cewa momma ke muguwa ce, ki barni na ganta ina sonta tana da kyau.
Ran momma ya k'ara 6aci afusace ta mik'e ta finciko Teema daga jikin barrister A, taja ta kamar kayan wanki ta kaita d'aki ra rufe tadawo ta kalle zee-zee da meena da ke tsaye wuk'i-wuk'i ta daka masu tsawa, nace ku 6ace min da gani shasshashu yaran kawai kun zo za ku takurata.

"Da gudu suka nufi bedroom d'insu, duk abinda take ko ci kanki Aliyu bai ce da ita ba, za ka ma dauka baya cikin sitting room d'in.
Hankalinshi kwance ya ce momma ga wifey ta zo yi muku bankwana, saboda na gayamata gobe da safe za ku koma Abj.
"Yak'arasa magana cikin halin ko in kula d'inan.
Duk cikin zanceshi kalmar wifey ce tafi k'onawa momma rai, jin take kamar ya soka mata mashi a k'ahon zuciya.
"zuciyarta kamar za ta fad'o k'asa tana murmushin dole ta ce, sannu daughter da fatan kina kulamin da yarona?"
Kinsan ba son aure yake yi ba dole ne akayi masa, idan bakya bashi kulawa komai zai iya faruwa, dole ki zage dantse ki bashi kulawa ta musanmman ko Allah zai sa kisami fili koda d'an k'ank'ani ne a farfajiyar zuciyarshi.

"Duk sanyi da ke falon bai hanawa barrister A shar6ewa da gumi ba, atarihin rayuwarta ba'a ta6a ci mata fuska a wulak'antata irin wannan ba, zuciyarta har tuk'uk'i take yi mata.
"Gani shirme da momma take yasa Aliyu ya yi sauri mik'ewa ya isa wurin barrister A ya rik'o shoulder ta ya mik'arda ita tsaye, yana kallon cikin idanuwanta.
"Gani yadda suka canza kala tausayinta ya kamashi yasan momma ta wulak'antata ba kad'an ba.
"Wifey mu je upstairs parlour ki gaisa da Daddy!
Har suka takala steps yana rik'e da ita momma tabi su da mugun kallo tana kintsa mugun nufi akan barrister A.

Sosai Daddy ya tar6eta yasaki jiki sai janta da fira yake, yana tambayarta akan abinda ya shafi aikinta, hakan yasa tasaki jikinta ita ma tana bashi amsa, nan take taji k'aunar dattijo ta cika ciki da wajen zuciyarta.
Fuskar Daddy dauke da murmushi ya k'ara duban barrister A ya ce "Da fatan ba dai wata matsala atsakaninku?"

"Cike da kunya ta girgiza kanta ta ce ba komai Daddy Alhamdulillah muna zaune lafiya.
"Masha Allah haka nakeso ji, ayi ta hak'uri da kuma biyayya don a cigaba da samun zaman lafiya.
Insha Allah Daddy mun gode Allah yak'ara girma da nisan kwana.

Daddy yasaki murmushin jin dad'i zuciyarshi cike da farin ciki ganin d'anshi ya mallaki iyali kamar kowa yanzu kam, hankalinshi ya kwanta sai kuma addu'a samun zuri'a dayyaba"
"A shagwa6e Aliyu ya turo baki ya ce uhm.....Daddy tun dazu da ita kadai ka ke fira ni ka wareni, kamar ba kasani ba.
Dariya Daddy ya yi kafin ya ce kadai ba ka rabuwa da rigima gadanga, ba ka gani ita ce bakuwa ko ba kasan bako rahama ne ba dole a girmamashi?"
"Sake turo baki ya yi ba wani nan Daddy nagano so ka ke ta kwace min fada awurinka.
Ba daddy kadai ba hatta barrister A saida ta dara.
Sosai sagarta Aliyu ya burgeta k'ato da shi yana shagwa6a, ta tuna yadda ita ma take yiwa Abbanta, duk girman mutum a gaban iyayyenshi k'aramin yaro yake komawa.
"Amina kina ji na da wannan rigimame mijin naki ko?"
Sadda kanta k'asa tayi cikin sanyi murya ta ce rabuda shi kawai Daddy ai ya riga yaci lokacinshi, a wurinka yanzu lokacina ne.
"Shigowar momma ya katsi musu nishadinsu, ko zaunawa bata yi ba ta ce kai Sultan tashi ku tafi gida babu kyau mace tayi sallar magarib ba k'ofar d'akinta ba.
Mun gode da ziyara ku gaida gida.
"Daddy ya daure fuska ya ce korarsu ki ke yi?"
Wai kin ma basu ruwan sha?"
Kafin ta bashi amsa Aliyu ya mik'e da sauri ya ce Daddy bari mu wuce Allah ya tsare hanya ya kai ku lafiya sai mun zo.
"ita ma mik'ewa tayi tai musu sallama tafice Daddy ya dauko bundle na 'yan one thousand ya mik'awa Aliyu gashi ka ba wa matarka, mun gode Allah ya ba ku zaman lafiya, Allah yak'are ku da sharrin mahassada.

"Amin Daddy cewar Aliyu ya juyo wurin momma ya ce mun tafi.
Ku gaida gida.
Tafada kamar za tayi bindiga.
"Koda ya fito tuni har ta shiga mota shi ma ya shiga Isah ya ja motar suka tafi.

Akan hanyarsu ya doura mata kudin da daddy ya bata akan cinyarta, ya ce inji daddy ya ce abaki.
Nagode Allah yasaka mishi da alkhairi

Amin!
Yafad'a yana kallonta kauda fuskarta tayi tana murmushi k'asa-k'asa.
Suna isowa gida ta wuce sashen tayi wanka had'e da alwala saida ta sallace sallar isha sannan ta tashi, ta shirya cikin Indonesia straight silk gown ta yane kanta da scarf, ta sauko downstairs parlour bata jima da zama ba ya shigo sanye da farar jallabiya mai gajeren hannu.
"Sannu da zuwa!
Tafad'a cikin cool voice.
Yauwa Yafad'a batare da ya kalleta ba ya cigaba da cewa idan kina jin yunwa akwai abinci akan dining.
"Daga haka ya haura upstairs yabarta da kallon bayanshi, girgiza kai tayi taji koda yunwa za ta kasheta ba za ta ci abinci ba gara ta kwana da yunwa.

"Kitchen ta wuce ta had'a coffee ta shige bedroom d'inta tana gama shan coffee, tayi brush tabi lafiyar gado saidai da kyar tasami bacci sakamakon yadda tunanin momma ya rufeta ga kuma na uban gayya, ita kam ta shiga uku wannan wane irin aure ne tayi?"
***""****""***
Washe gari sai misalin k'arfe 11:14am tafito downstairs parlour, waya take yi da wani client d'inta ya shigo sanye da white sport wears k'afarshi sanye da sneakers farare, dawowarshi kenan daga jogging.
"Ina kwana Yalla6ai?"
Ya tsaya cak....yana kallonta girar ido d'age daga bisani ya ce ya akayi jiya ba kiyi dinner ba?"

Jeeddah Aliyu
[7/27, 12 AM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDA NA KUD'I NE IDAN KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*20*

Murmushi tayi kafin ta ce bana jin yunwa shiyasa ban ci ba, amma before in kwanta nasha coffee.
"Ta6e baki ya yi had'e da mak'e kafad'a irin I don't care d'inan ya k'arasa haura steps.
Ta bi shi da kallo tana tausayin kanta yadda ta tsunduma soyayyar mutume da bai ma san tana yi ba.
Ta rafka d'an uban tagumi, k'amshin turarenshi yadawo da ita natsuwarta ta bishi da kallo har isa dining area bata dauke idanunta daga akashi ba, sosai dressing dinshi ya burgeta white long sleeve had'e da white trouser yasaka. "Sumar kanshi tasha gyara ya yi masifar yi mata kyau.
"Saida ya zauna sannan ya waigo wurinta ya yafito da hannunshi, jikinta asanyaye ta mik'e ta nufo wurinshi.
"Ya kalleta da girar ido d'age ya ce dai barrister ko yanzu dinma bakyaji yunwa?"
Murmusa had'e da zarar plate tayi serving dinshi, sannan ta zauna ta yi wa kanta serving.
"Suna cin abinci tana satar kallonshi afakace, yi ya yi kamar bai ganta ba.

"Yana gani za ta dame shi da kallo yasa ya ce Barrister ki ci abinci kada ya yi sanyi, ko abinci ne bai miki dad'i ba?"
Sosai taji kunya ta rufeta, ta shiga cusa chips d'in tana taunawa kamar mai cin mad'aci, kafin ta ankara ya mik'e yabar mata dining d'in.
Ajiye fork tayi ta talla6e kumatunta tayi zurfi atunani, taji sauti muryarshi yana cewa ni zan fita. Da kyar iya furta adawo lafiya!
Yajuya abinsa ta bishi da kallo.
***""***""****
Misali k'arfe 8:00 na dare bayan sun kammala dinner, ta tattara plates da suka yi using ta kai kitchen ta wanke.
"Koda tadawo downstairs parlor ya fice, shiru tayi tana nazarin wayar da ta yi da barrister Z d'azu da safe.

_Inda take cewa Bebs ki cire kunya da miskilanci ki nemi kusanci da mijinki, shi namiji ne ko a yanzu yana da damar auro mace har uku, sa6ani ke kinga kenan kece a wahala ki yi wa kanki fad'a bebs tun kafin lokaci ya k'ure miki, karki mata ke mace ce Allah ya yi miki ni'imomi da yawa da za ki janye hankalin d'a namiji da su karki yi wasa da damarki, kafin ku wuce Abuja ki yi k'ok'ari ki nemi kusanci da shi_

Ajiyar zuciya tayi had'e da dafe k'irjinta, daga bisani ta nufi bedroom d'inta ta sauya kayan jikinta zuwa Indonesia gown mai santsi gaske talafe a jikinta, ita kanta da ta kalle kanta da mirror saida ta firgita sakamakon yadda gown d'in ta baiyana surorin jikinta.

"Arabian perfumes tayi amfani da su saboda sun fi k'arfi da jan hankali, tasaki gashinta ya sauko har gadon bayanta ta yanne kanta da d'an siriri mayafi.

"Tasaka wasu slippers masu taushin gaske a k'afarta

Kai tsaye ta wuce kitchen ta had'a mishi coffee sannan ta nufi falonshi da ke upstairs, tun kafin takarasa take jin sautin muryarshi, tasan waya ne yake yi.

"Da sallama tashigo ya juyo ya kalleta ita ma kallonshi, tayi kafin ta kauda kanta ya yafito ta da hannunshi ya yi, alamar da ta k'araso.

Ta ajiye mug din coffee akan center table da ke gabanshi, ta nemi sofa ta zauna bai wani jima yana waya ba ya ajiye.

"Ya dauki coffee yana sha ahankali yayin da ta sadda kanta k'asa tana wasa da gefen gyaleta, shiru ya biyo baya karar TV kawai ka ke ji sai kuma zuciyar barrister A da ke bugawa very fast.

Ya canza channel zuwa idan ake haska movie na horror, satar kallonshi tayi anan ta ga hankalinshi na kan movie d'in hakan yasa ita ma ta maida hankalinta ga Tv.

"Tuni hanta cikinta yafara kad'awa gani yadda zombies ke wasa da jinin bil-adama, ta runtse idanunta gam....
Ita kam sam bataso irin movies dinan tsorata ta suke yi.

"Kallonta ya yi ya ta6e baki ya cigaba da kallonshi, can yasake kai dubanshi wurinta still idanunta a rufe ruff....ya yatsine fuska kafin ya ce barrister tashi ki koma bedroom dinki kada ki yi bacci anan.

Sai lokaci ta bud'e idanunta ta girgiza kanta muryarta, asanyaye ta ce ba bacci nake ji ba.

"Bai ce da ita uffan ba ya cigaba da kallonshi sai around 11:20pm aka gama film d'in yana k'ok'arin tashi ta kalle shi ta ce sai da safe Yalla6ai.

Batare da ya kalleta ba ya ce "sai da safe.
kafin ta k'ara wata magana sai ya mik'e yabar mata falon ya nufi bedroom, ta bishi da kallo tana sanyaye murmushi.
Ita da ta zo mashi fira ya tafi ya barta da gadin falonshi, ta d'an jima zaune tana zance zuci

daga bisani ta mik'e ta koma nata sasshe, da kyar bacci ya yi nasarar dauke ta.
"Tabbas akwai jan aiki agabanta ba kad'an ba.

"Shi ma ta6angareshi yana kwance zuciyarshi cike, da tunani abinda yafi tsaya masa arai duk yadda barrister A tayi kwaliyya sai ta burgeshi, zai dauki dogon lokaci kafin ya manta da kwaliyyar ta ta.
Uwa-uba mayyen turarenta da ke addabarshi muddin ya shak'i k'amshinta sai ya tsince kanshi a wani yanayi wanda shi kanshi ya rasa gane na menene.

"Washe gari da safe suna zaune a dining table tana serving d'inshi, ya d'ago ya dubeta afakace ba shiri ya dauke kanshi zuciyarshi na bugawa da k'arfin gaske, sakamakon yadda tayi mishi kyau kamar wata aljana.
"Ya sadda kanshi k'asa yana cin abinci ba don yana jin dad'inshi ba, adaddafe yaci abinci yana kammalawa yabar dining area ta bishi da kallo har ya haura steps idanunta na kanshi.
"""****"""****""""
A kwana atashi asarar mai rai gashi yau kusan sati biyu kenan da auren Aliyu da barrister Amina.
"Da Yammacin ranar talata barrister A tana tsaye a kitchen tana gyaran fruits za ta had'a fruits salad, taji shigowarshi saida ta kammala had'awa ta zuba mishi nashi a bowl tasaka ice cubes sannan ta nufi falonshi.
Zaune ta sameshi yana operating waya jin motsinta da kuma k'amshin fittinane turarenta, da ya bigi k'ofufin hancinshi ya haddasa masa d'agowa da kanshi, ya kalleta ya kauda fuska ya cigaba da dannar wayarshi, ga alama chat ne yake yi.
Ta ajiye bowel d'in hannunta akan center table.

Sannan ta isa ga kujerar da ke facing dinshi ta zauna tana mishi sannu da dawowa.
Ya amsa batare da ya d'ago da kanshi ba ya kalleta.
Ta kalleshi sosai kafin ta ce "Yalla6ai ga fruits salad na kawo maka bansani ba ko kana da sha'awarshi.

Asanyayye yai murmushi ya d'ago suka had'a ido cikin tsadaddiyar muryarshi ya furta nagode! Daga haka suka yi shiru shi yana dannar wayarshi ita kuma tana aikin kallonshi, can dai ya d'ago tai sauri kauda kanta.
Ya yi murmushi saboda ya ganota sarai....kallonshi take yi ya dauki fruits salad d'in yana sha yana kad'a kai alamar ya yi mishi dad'i.
"Yana gama sha ya mik'e ya shige shi bedroom ya barta zaune.
Da tagaji da zama ita kadai ta koma nata falo.
**"""***"""****
Misali k'arfe 10:00 na dare fitowarta daga wanka kenan, tana daure da towel wanda ko cinyoyinta bai gama rufewa ba. Barrister Z ta kira ta ta duba email d'inta akwai sak'o da ta turo.
"Laptop d'inta ta dauko da ke aje akan bedside drawer, ta nemi gefen gado ta zauna ta shiga duba email d'in ta shagala sosai har rabin towel d'in ya zame daga k'irjinta rabin boobs d'inta a fili.

"Jin an murd'a k'ofar d'akinta yasa ta tsorata da sauri ta juya Aliyu tagani tsaye ya yi folding hannayenshi a k'irji, mayyun idanuwanshi ya zuba mata masu kama da na mai jin bacci, kamar mai koyo magana ya ce coffee za'a bani.

"Ta gyad'a kai alama amsawa sai dai kuma tana matuk'ar jin kunyar yadda za ta, tashi da wannan d'an towel a gabanshi.
A tunaninta ficewa zai yi sai ta tashi sai taga sa6anin hakan.

Jeeddah Aliyu
[7/27, 12:01 AM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

Not edited!

*21*

Ya gyara tsayuwarshi ya kuma rik'e handle d'in k'ofar, ya cigaba da kallonta ta gefen ido.
Ta waiga gefenta ba wani abin da za ta rufe jikinta da shi.
Can Allah ya taimaketa ta hango hijabinta na sallah akan praymat, ta d'an sosa tsakiyar kanta, cikin tsananin jin kunya yadda za ta tashi gashi ya tsareta da brown eye's dinshi.
Gani bata da niyar tashi yasa ya ce I'm waiting barrister!
Ta d'an kalle shi cikin jin kunya ta ce "Yalla6ai ka tsaya a bakin k'ofa ban san yadda zan yi in fita ba, ina jiran ka janye sai in tashi"

"Dama idanuwanshi na kanta ya dan murmusa sannan ya juya ya fice, daga d'akin.
Gani haka yasa ta mik'e cikin sauri ta isa wajen praymat, ta dauki hijabinta ta sanya ya sauka mata har k'asa, sannan ta fice.
"Ta had'a coffee a mug ta nufi falonshi a tunaninta yana nan falo, sai taga sa6anin hakan.

"Dole ta wuce bedroom d'inshi zaune ta sameshi akan resting chair, asanyaye cikin girmamawa ta runsuna ta mik'a masa coffee.
"Garin amsa by mistake ya had'a da hannunta, wani irin shock ya ja su, sai kace electric shock jikinta ya dauki rawa cikin zafin nama ya rik'e mug d'in da coffee ya zube mishi a jiki. kallon k'asan ido ya yi mata ta kauda fuskarta, had'e da furta "I'm sorry!.
Ki zauna mana ki yi tsaye!
Yafad'a yana kallon gefen face d'inta.

Girgiza kai tayi had'e da cewa bacci nakeji idan akwai wani abu da ka ke buk'ata, ka fad'a nayi maka kafin na kwanta.
"Ya kai mug d'in coffee abakinshi ya d'an kur6a ya kalleta a tsanake, ya ce ki je ki gyaran min bed tunda komai sai na rok'e ki.
Sosai ta dube shi kamar ba za ta yi magana ba, sai kuma ta daure ta ce "Ba ka bani fuskar yin hakan bane, da ba sai ka rok'a ba.
D'auke kanshi ya yi daga barin kallonta ya cigaba da shan coffeenshi, kamar ba zai ce komai ba ganin yadda take tsaye yasan tana jiran jin ta bakinshi ne.
Duk mace tagari tasan responsibility da yake kanta.
Uhm....Yalla6ai karka jefe ni da magana mana sanin kanka ne, komai da mazauninshi.
"Haka hasasshenki ya baki za ki iya tafiya idan gyara d'akin nawa zai ba ki matsala, dama girl's like you ba abinda ku ka iya sai kwaliyya, always cikin makeup kamar masu zuwa za6e miss world.
"Ya salaam! Sam bata yi tsanmani jin irin wad'annan maganganu daga bakinshi ba, shiyasa taji wani irin tai shiru tana kallonshi da mamaki shinfid'e akan fuskarta.
Gani yadda take kallonshi yasa cikin low voice "ya ce please you can leave barrister!
"Ta cire kai ta kalle shi coffenshi kawai yake sha, kamar ma ba da ita yake magana ba.
Sosai hakan ya 6ata mata rai sai kawai ta juya tabar d'akin, batare da tasake cewa komai ba, saidai kuma ta shiga tunanin me yake nufi da _girl's like her ba su iya komai ba sai makeup which means yana kallonta amatsayin wacce bata iya komai ba shiyasa ya hanata fara girki_

Ta isa bedroom d'inta zuciyarta cike da damuwa na rashin sani manufar idan maganarshi ta dosa.
"Tabbas Aliyu ya cika cikakke d'an reni hankali wato yana jira sai ta kawo mishi kanta, to kuwa tabbas za ta shayar da shi mamaki.
Har ta kwanta sai kuma ta ga rashin dacewar abinda tayi ko ba komai, yana matsayin mijinta yana kuma sama da ita dole ta yi mishi biyayya.
Zubur.....ta mik'e tsaye ta bud'e closet ta dauki wrapper ta daura akan sleeping dress d'inta.
Ta murd'a handle gabanta na fad'uwa yana nan zaune idan ta bar shi, sai dai yanzu yana operating wayarshi.
kallo d'aya ya yi mata ya kauda fuska, ba ta ce da shi uffan ba ta cire bedsheet d'in ke shinfid'e duk dai bai yi wani dirty ba, ta shinfid'a new one ta kunna water burner ta zuba perfume mai k'amshi strewberry, tuni d'akin ya dauki k'amshi.
Ta shiga tattare files d'in da ke zube a k'asa ta adana su ciki bedside drawer.
Ta waiga ta kalle shi "ta ce Yalla6ai  na kammalla gyara gadon ko akwai wani abu da ka ke buk'ata?"

Harara ta yi ya da brown eye's d'inshi yana yatsine fuska, "ya ce ba fushi ki ka yi ba waye shawarce ki ki ka dawo?"
"murmushi ta yi kafin ta ce, ba fushi nayi ba zani naje na dauro.
Uhm....za ki iya tafiya nagode!
Sai da safe!
Tafada had'e da ficewa.
***""****""""*****
Washe gari suna kammalla breakfast Aliyu ya koma d'aki ya yi wanka, sai gashi ya fito cikin white three quarter as usual had'e da armless shirt, lokaci tana zaune a falonta ya shigo ya nemi kujera ya zauna, cikin husky voice "ya ce ki shirya kayanki gobe za mu wuce abuja nagaji da garinan.
"Kamar za ta yi kuka take kallonshi har ga Allah bata saka rai da wuri za su wuce abuja ba.

kinji koh?"

Ya katse mata zance zucci.

Naji!

Tafad'a asanyaye.

Sai ki shirya zuwa anjima mu je ki yi wa su Ummi bankwana.

"Nan take tasaki murmushi saboda tayi kewar gida ba kad'an ba.
Ya mik'e yabar falon ta bishi da kallo tana murmushi a k'asan zuciyarta kuma ta ce "A dai juri zuwa rafi wata rana tulu zai fashe, insha Allah za ka shigo hannuna sai na sauke ma miskilanci da girman kai.

"Mik'ewa tayi ta nufi kitchen kasancewar akwai kayan abinci da duk wani abu da za'a buk'ata wurin girki, yasa ta yi decided ta nuna mishi bata cikin girl's d'in da yake tsanmani.
"Aliyu na fita direct garden ya wuce saboda yana buk'atar fresh air, newspaper na leadership ne a hannunshi yana dubawa.
"Cikin k'ank'ani lokaci gidan ya dauki k'amshi girkinta, ta had'a fry rice da pepper chicken, with comslow sai juice na coconuts & pineapple.
Tun daga garden ya keji jiyo k'amshi girkita, da yake kafin tafara girkin ta bud'e windows.
"Koda k'arfe 1:30pm ta yi ta shirya table ta koma d'akinta ta yi wanka ta shirya tsaf cikin California authentic gown mai open neck tasaka bohemian sterling earring, sallah ta yi sannan ta yane kanta da scarf wanda ya yi match da gown d'inta.
Ta sanya ballerina flats shoe, sosai tayi kyau na ban mamaki sai k'amshi take yi.
Ta fito ta zauna bata jima da zama ba sai gashi yana saukawa daga upstairs, bai zauna a falo ba direct ya wuce dinning area ya kagara ya ci abinci nata ya ji menene yake k'amshi a cikinsa.
Tasowa tayi ta dauki plate tayi mishi serving, ta mik'a hannu ta janyo warmer da pepper chicken yake ciki, yadda ta ware hannunta yasa rigarta ta sauka a fuskarshi, ya shak'i k'amshin jikinta wani shauk'i na ban mamaki ya ziyarce shi.
Ya d'ago da kyar ya Kalle irin shigar da ke jikinta, ya yi sauri dauke kanshi, ya juya yana kallon TV da ke manna a bangon dinning.
Ta ajiye plate agabanshi ya dauki spoon yana ci a yangace, yana mamaki sam bai dauka ta iya girki har haka ba.
Kamar ya tambayeta ya akayi ta kware da girki har haka, mai dad'i saboda ya ji dadin abincinta ba kad'an ba.
Fasa tambayarta ya yi saboda baya so reni, atunaninshi tambayarta zai iya kawo reni a tsakaninsu.
Sosai ya ci abinci musanmman juice duk lokaci da ya kur6a shi sai ya lumshe ido, afakace take satar kallonshi duk abinda yake yi.

Taji ya yi bala'in burgeta.
Yana gama cin abinci ya mik'e ya koma falo, ta tashi tabi bayanshi.
har k'arfe 4:30pm tayi bata ta ji ya ce ta taso su tafi ba, gashi kusan sau biyu tana komawa bedroom tana gyara makeup d'inta.
Gani tayi ya kwanta akan kujera, ya minmik'e k'afafu, yana lumsashe idanu ga alama bacci yake so yi.
"Yalla6ai ba dai bacci bayan la'ssar za ka yi ba?"
Ya bude idonshi d'aya yayin da d'ayan yake arufe, ya kalleta yana murmushi sosai yana yin da yake kallonta ya haddasa mata fad'uwar gaba, ba shiri ta dauke kanta da bari kallonshi.

Shima ya dauke idanuwanshi daga kallon nata yana fad'i "Ke dai ki ce kin Kagara ki je gida ki ga Abba.
'Yar siririya dariya tayi mai ban sha'awa tsayawa ya yi yana kallon bakinta yanda sauti dariya yake fita daga cikin.

"Ta tsagaita da dariyar ta ta, ta ce banida laifi Yalla6ai kaine ka saka min ra'ayin son zuwa

gida, don haka bacci bai ganoka ba ka zo mu tafi tun kafin na fara tsandara maka kukan ido d'aya.

Sosai furucinta na k'arshe ya bashi dariya da yake shi ba gwanin dariya bane, sai kawai ya yi murmushi mai sautin gaske kafin ahankali ya ce "oh.....haka ne?
Ai kuwa kin d'ebo ruwan dafa kanki don sai kiyi min kukan ido d'aya, za ki ga Abba.

"Dauke kanta tayi tare da rufe bakinta da tafi hannunta.
Da gaske fa sai kin yi kukan ido d'aya.
ya k'arasa magana yana turo baki kamar k'aramin yaro.
"Ba shiri ta taso ta durk'usa gabanshi ta had'e hannayenta wuri d'aya ta ce "don Allah Yalla6ai ka rufa min asiri da wasa nake.
"Murmusawa ya sake yi kafin ya mik'e batare da yasake magana ba, ya ra6ata ya haura upstairs ya sauya kayan jikinshi zuwa shadda as usual fara tass......har da saka hula zanna bukar.
k'afarshi sanye da loafers shi ma white in colour.
Yana fitowa ta ragu da d'an gudunta ta dauka handbag, sai murna take za ta gida.
Parking lot suka nufa suna tafiya side by side kallo d'aya za ka yi musu kagano sunyi bala'in dacewa da juna.
"Tun kafin Isah ya gama parking ta balle k'ofa za ta fita, karaf ya rik'o palm d'inta yana mata shegen kallon nan nashi na k'asan ido.
Batasan lokaci da ta rausayar da kanta tana kallon k'ofar shiga apartment d'insu, wannan shi ake kira ga k'oshi ga kwanan yunwa.

"Hey.....barrister stop act like small girl, kina gudu kamar wata 'yar baby.
"Dauke kanta tayi ta ji wani irin mugun kunya ya lullu6eta, ya saki hannunta tak'arasa fita.
Tana fitowa khalil da Khalid da ke fitowa daga cikin gida suka hangota, da gudu suka rungumeta sai ihun murna ganinta suke, Khalid ya d'agata kamar 'yar baby sai juye yake da ita yana sauke ta Khalil ma ya d'agata, k'arshe ya direta ya kar6i handbag d'inta suka nufi cikin gida.

"Aliyu da ke tsaye a jikin mota ya yi folding hannayenshi a k'irji, sai kallonsu yake yana murmushi, har sun yi kusan shigewa cikin gida sai ya ga twins d'in sun juyo yayin da barrister ta shige ciki.

Wurinshi suka nufo suna murmushi, khalil ne yafara mik'a masa hannu yana fad'i "sannu da zuwa Yalla6ai!
Uhmm......sannunku twins ina kallonku za ku karya min mata.
Dariya suka yi shima yana taya su ta hanyar murmushi, shoulder Khalid ya dafa ya ce twins ya karatu?"
Alhamdulillah!
Suka had'a baki.
Mu shiga daga ciki Yalla6ai kada matarka ta tuhume mu mu bar ka a tsaye.
"Shiru Aliyu ya yi yana shafa geminshi, jerewa suka yi zuwa cikin gida.
A babban falo suka tararda ummi barrister A tana kwance a jikinta, duk ta makalk'aleta.

Shigowar Aliyu yasa ta tashi a kunya ce sai faman gyara veil d'in kanta take yi, gaida Ummi ya yi ta amsa cikin fara'a barrister A ta mik'e ta shiga kitchen da kanta ta kawo mishi ruwa da lemo duk tasan ba sha zai yi ba.
sallama ya yi da Ummi akan sai k'arfe 8:00pm zai dawo picking d'inta, sosai hakan ya yi mata dad'i har k'ofar fita daga falo ta rakashi.
****""*****""""****

Kamar yadda ya yi alk'awali 8:00pm a gidan tayi mishi, yana tsaye jikin mota sai ga khalil ya fito daga cikin gida za shi parking lot Abba ya aike shi ya dauko mishi wasu documents a mota.
Shaking hands suka yi kafin ya dauko aike da aka yi mishi ya jagorance shi suka shigo cikin gida.
"Gaba d'aya ahalin gidan suna zaune, ya durk'usa har k'asa ya gaida Abba, cike da fara'a Abba ya mik'e masa hannu cikin jin kunya Aliyu ya yi musabaha da shi.

Nasiha Abba ya shiga yi musu akan zamantakewar aure, sai kuma dadd'a k'ara bashi amanar barrister A.
"Hakan yasa Aliyu ya ji jikinshi ya yi sanyi.
Gaba d'aya har Abba suka rako su wurin motasai kuka take, Abba ya rik'e hannunta kamar ba zai saki ba, ta gefen ido Aliyu yake kallonsu "the thing looks very funny musanmman yadda Abba ya yi da idanu kamar shi ma zai yi kuka.
Saida suka ga fitar su daga gidan, sannan suka juya cikin gida.
Suna tafiya tana share 'yan hawayenta ji take kamar ta ce ba za ta bi shi Abuja ba yabarta Yola, ta dinga gani parents da siblings d'inta.
"Ya waigo suka had'a ido ya daure fuska tamau....kaman ba shi bane yanzu nan ya gama murmushi ba, ya fito da handkerchief daga aljihunshi ya mik'a mata yana cewa common wipes that tears before I loosing my control na bige miki baki, kanki aka fara aure da za ki cikawa mutane kunnen I hate cry in my whole life" musanmman irin naki na rashin dalili.

"Hannunta na rawa ta kar6i handkerchief ta goge fuskarta, har da fayyace su majina ya yatsina fuska ya d'an buge shoulder ta ya ce k'azamar banza wannan handkerchief yana zamanki, don ni ba abinda zan yi da shi.
Kunya ya lullu6eta har suka iso gida ko kwakwaran motsi takasa.

Har ta juya za ta shiga d'akinta ya tsaida ta ya ce "ki shirya luggage dinki sai ki zo ki shirya min nawa, banaso mu yi latti morning flight za mu bi.
"Ta gyad'a kanta sai kusan 10:18pm ta gama shirya kanyata, ta gaji sosai dole ta wuce bathroom ta watsa ruwa masu zafi ko za ta wartsake daga gajiya.
"Cotton night gown tasaka mai spaghetti hands pink colour, ta sauka iya gwiwarta ta zura hijab mai hannu yana ja da k'asa ta nufi d'akinshi.
Tana tura k'ofa yana tsaye jikin window daga shi sai wando sleeping dress bai saka riga ba, har ta juyo za ta fita ya ce "ke....banaso shirme zo ki yi aikinki nida gidana ba za ki hanani shan iska ba.
A kunyace tadawo ta bud'e closet tana fitowa da suits dinshi tana sakawa a trolley, ahankali

take satar kallon jikinshi cikinshi a shafe ga six packs dinshi a jera,  muscles d'inshi a murd'e Aliyu giants man ne yana cikin maza masu inverted triangle body, ta Kalle yadda wandon ya zauna a waist dinshi kamar wani modeling.

"Yasaki curtain ya zauna akan resting chair ya dauki system d'inshi, yana dan-dannawa ita kuma tana aikin had'a mishi luggage.

"Gyagyad'i tafara bata ankara ba bacci ya yi wuf....da ita hannunta rik'e da boxer dinshi Hankalinshi ya dauku sosai ga aikin da yake shiyasa bai lura da ita ba, tsawon lokaci ya dauka yana sarrafa laptop atunaninshi ta gama had'a kayan ta fice sai da safe ne kawai bata yi mishi ba.

Doguwar hamma ya yi had'e da mik'a waigowar da zai yi ya ganta zaune a k'asa ta kifa kanta a gefen gado, ga boxer d'inshi akan fuskarta dad'in bacci yasa ta ya6a boxer akan fuskarta.

Zaro idanuwanshi ya yi cike da mamaki ya tashi ya nufi wurinta, ahankali ya ciro boxer ya k'ura mata ido baccinta take yi hankali kwance.
Bai san lokaci da ya tintare da dariya ba abinda bai cika yi ba.

Jeeddah Aliyu
[7/27, 12:01 AM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903
*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA  GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

*22*

Ya shiga bubbuga hannunta yana kiran sunanta ahankali, ko motsawa ba tayi ba.
  Cigaba da tashe ta ya yi hey.....barrister wake up go to your room...hey....hey...wake up! Barrister nace ki tashi ki tafi d'akinki nace ki tashi mana don't tested my patience.
Ya k'arasa magana cikin shouting firgigit tayi tana kallonshi, sai kawai ta sulale akan tiles ta cigaba da bacci abinta.
Omg!
Yafad'a dafe da goshi duk yadda yaso ya tashe ta abin yaci turu dama barrister akwai nauyin bacci.
   "Tilass....ya dauketa cak ya aza akan gado ahankali ya cire mata hijabin jikinta, gashinta yarufe mata fuska, ya tattare shi ya mayar mata da shi baya ya yi tsaye yana kallon yadda numfashinta ke sauka k'irjinta na up and down, boobs d'inta na wani d'agowa ga shatin  two nipples d'inta da ke cikin night gown kamar su tsokane mishi ido.

Gogan naku baisan lokaci da ya hadiye yawu ba, wannan shine karo na farko da yata6a k'arewa mace kallo.
 Da sauri ya runtse idanunshi ya shiga waresu ahankali, he was still staring at her ya durk'usa gefen fuskarta wearing a killer smile, wanda shi kanshi ba zai ce na menene ba.
Ahankali yasa two soft hands d'inshi ya d'an gyara mata kwanciyarta.
   "Ya zagaya gefenta ya kwanta ya dauki three pillows ya yi musu tsakani, kamar jira take ya rufe idanunshi tafara wani shegen snoring a firgice Aliyu ya bud'e idanuwanshi, don tabbatar ita ce take snoring ya lek'a fuskarta duk da d'akin diff light ne bai hanashi, hango yadda snoring d'in ke fita daga bakinta ba.
A tsoro ce ya janye yana dafe goshi mik'ewa ya yi ya nemo auduga ya toshe kunnayenshi, ya ja duvet ya rufe jikinshi can cikin bacci ya ji ta fincike duvet d'in ta rufawa nata jiki, hakan ba k'aramin k'ona mishi rai ya yi ba.
Afusace ya fizge duvet ya girgiza shoulders ta ya ce ke tashi maza ki barmin d'akin.
Ba zai yu ki hanani bacci ba nida d'akina.
wani juyi ta yi ta cigaba da baccinta.
"Mtsss....ya ja tsaki yana hararata ya kwanta can tsakiyar dare har baccinshi yafara d'adi yaji wani shegen kick a d'uwawunshi, ya tashi atsoroce cikin angry face yake kallonta.
   "Ya rabbi help me this girl gonna kill me, yafad'a dafe da goshi ya sauka daga gado ya jefa mata bargon yana fad'i gashinan ki cinye duvet d'in mayya kawai.
Kan resting chair ya koma ya kwanta sannan ya sami bacci saidai ba mai dad'i ba
Kiran sallar asuba ne ya tashe shi, ya tashi yana dafe goshi, sakamakon rashin samu wadattace bacci ya jawo mishi headache ya juya ya kalli kan gado sai sharar baccinta take yi.
Ta rungume pillow a k'irjinta.

Dauke idanuwanshi ya yi daga kallonta, ya mik'e tsaye da kyar yana rangaji ya shiga bathroom.
Ya dauro alwala canza kayan jikinshi zuwa farar jallabiya, da farko har ya yi niyar ya yi tafiyarshi masjid ba zai tashe ta ba, sai kuma ya ga rashin dacewar hakan.
"Cike da mugunta ya zuba mata wani shegen duka a gadon baya, saida ta gantsare kafin tayi nasarar kwalla jahilin ihu mai barazanar doshen dodon kunne Aliyu.
"Da sauri ya fice daga d'akin yana murmushin mugunta.
Fitarshi yasa tadawo da natsuwarta ta fahimci idan take, sosai mamaki ya rufeta da ta tuna abinda ya kawota d'akinshi har bacci ya dauketa.
"K'ayattace murmushi ta yi ta d'an bige bayan k'eyarta, sai kawai take ji wani irin nishad'i ta jima sosai tana blushing  kamar wacce aka yi wa albishir da mallakar zuciyar Aliyu....lol.
Jin footsteps dinshi ya nufo d'akin yasa ta mik'e da gudu ta shiga bathroom, koda tafito har ya shigo yana zaune akan resting chair closing his two eye's ta kalle shi asanyayye kafin ta dauki hijab da praymat ta yi sallah, tana gama sallah ta ce "Ina kwana Yalla6ai?"
Ya bud'e idanuwanshi masu cike da bacci, saida ya yatsine fuska kafin ya ce banganshi ba.
Zaro manyan idanuwanta tayi masu kamar da an diga mata zaiba, tana kallonshi ba ki bud'e.
Kafin tayi magana ya katseta ta hanyar cewa tashi ki je had'a mana breakfast, idan kin kammala ki zo ki tasheni.
Ta mik'e tana murmushi ta nufi k'ofar fita ya bi ta da kallo, tana ficewa ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya.
Ya haye bed had'e da switch off d'in bulb.
Ga mamankinshi a maimakon ya yi bacci sai ya tsince kanshi da tunaninta, tsawon lokaci ya dauka kafin ya samu bacci ya dauke shi.
Tana bari d'akin ta shiga nata ta canza kayan jikinta, ta shiga kitchen a gaggauce ta had'a breakfast, ta shirya table, sannan ta koma d'akinta tayi wanka ta shirya tsaf.....cikin atamfar super exclusive d'ikin skirt and blouse kayan sun kar6i jikinta sosai tayi kyau na ban mamaki tayi dauri d'an kwali Zarah buhari, ta kammala komai sannan ta nufi d'akinshi, ta samu ya tashi har ya shiga wanka, ta isa ga gadonshi ta shiga gyarawa, tana cikin gyara gadon ya fito daga bathroom sanye da bathrobe ta dauke kanta daga gefen da yake tsaye, tana gama gyarawa ta fice daga d'akin.
misalin k'arfe 11:00 na safe suka bar gidansu zuwa Airports, Isah direba na sauke su ya yi sallama da Aliyu saboda zai shi yi driving motar barrister A zuwa Abuja.
"Lokaci da flight d'insu ya yi landing direban Daddy ne ya dauko su.
Tun da suka fito daga Airports take kallon hanyoyin da direban yake bi, har suka iso Ardo mansion.
Da gudu gateman da security d'in gidan suka iso wajensu, suna gaida su ta amsa fuska sake har ma da wani d'an siririn murmushi.
Ta fito daga mota tabi bayan Aliyu sun iso flat dinshi ya ciro keys ya bud'e k'ofa suka shiga daga ciki.
Gate man ya shigo musu da kayansu, cikin mintuna k'alilan ta d'anyi nazarin falon k'asa duk abinda ke ciki kama daga cushion har zuwa painting falon white colour ne, kamar dai yadda gidansu na Yola yake saidai wannan yafi na Yola had'uwa.

"Ki hau sama mana"

Muryarshi ta daki dodon kunnenta, ta juya cikin salon tafiyarta ta bi steps ta hau saman saidai ta ja ta yi tsaye sakamakon rashin sani wane daga cikin k'ofufin da ta samu ne, nata.
Bata jima da tsayuwa ba ya shigo ya ra6ata ya nufi wata k'ofa ya bud'e, ta bi bayanshi.
Nan ma parlour ne ya sha kayan alatu na more rayuwa.
"Ya nuna mata wata k'ofa can k'asan mak'oshi ya ce ga sasshenki anan, yak'arasa magana had'e da mik'a mata key, ya shige d'akin da take tunanin shine na baccinshi.
"Ta kad'a kanta ta bud'e falon ta shiga ta wuce bedroom, ta ajiye jakkarta da mayafi ta shiga gyara wurin saida ta gama, tanufi nashi ta gyara taji motsinshi a bathroom, agaggauce ta shiga gyara d'akin koda yafito har ta kammala ta fice, ta gyara mishi falo, sannan ta sauka k'asa nan ma ta gyare shi tass....ta shiga kitchen ta yi nazarinshi nan ma ta tsafta ce shi, gaba d'aya gidan ya dauki k'amshi na fitar hankali.
Ta koma d'akinta ta yi wanka ta had'o da alwala, da yake lokacin sallar azhar ya yi ta yi sallah.
Sannan ta tsantsara simple makeup, ta dauko luggage d'inta ta ciro Arabian gown purple colour, tasaka tayi rolling da white veil.
"Tana cikin fesa perfume ya turo k'ofa ya shigo shima ya sauya kayan jikinshi, zuwa white chino trouser had'e da mandarin long sleeve, ya nad'e hannayen rigar.
"K'amshinta ya had'e da nashi ya k'ara k'amsasa d'akin.
Kallo d'aya ya yi mata ya dauke kai, tayi mishi kyau ba k'adan musanmman da tayi rolling da white veil favorite colour d'inshi.
"Mu je flat d'in momma ki gaisa da su ga alama basu san mun iso ba.
Yana k'arasa magana ya juya ta biyo shi abaya tana k'arewa compound d'in gidan kallo.
A downstairs falo suka iske momma da Zee-Zee momma na waya yayin da zee-zee ke kallon movie.
"Sallamar Aliyu ya dawo da hankalinsu akansu, zee-zee ta tashi cikin farin cikin tayi hugging barrister A.
Lokaci da momma tayi arba da barrister ta ji gabanta, ya yi mummunan fad'uwa da had'ye wasu mushirkai miyau.
"Barrister A ce tafara janye zee-zee daga jikinta, ta durk'usa ta gaida momma ta amsa cikin fara'a saboda tsabar makirci hadda su rungume barrister tana fad'i welcome to the family my daughter ya gajiyar hanya?"
Murmushin jin dad'i barrister A tayi duk tasan wannan welcoming da momma tayi mata bai gansheta ba
Aliyu ya nufi one sitter ya zauna ya yi crossing legs d'inshi, shi ma ya gaida momma ta amsa tana washe hak'ora.
"Sultan ashe kuna hanya?"
Uhm....!
Yafad'a kamar an mishi dole.
To miyasa jiya da dare da mu kayi waya ba ka fad'amin yau za ku zo ba?"
"Na manta ne!
Ya fad'a yana yatsina.
Kodai ka fad'awa Daddynka, ni ce da ka rena ba ka fad'awa ba?

Omg.....momma please banaso irin tambayoyin nan naki, sosai suke haifa min da ciwon kai. Ya k'arasa magana yana turo miki.

"K'atuwar harara momma ta wulga masa afakace, a fili Kuma ta k'ikk'iro murmushin dole ta ce haba gadangana don nuna damuwa na akanka laifi ne?"

"Wani shegen murmushi Aliyu ya yi kafin ya ce kai....momma na fahimci yau K'orafi ki ke ji, to Allah ya ba ki hak'uri.

"Zee-zee ta rik'o hannun barrister A zo mu tafi matar Yaya d'akinmu mu yi fira, wallahi ina cike da farin ciki zuwanki gidanan ba k'adan ba.

"Nasan ko Meenat idan tadawo daga school ta ganki, haukace mana za tayi, saboda tun lokaci bikinku bakinta bai huta da zance ki ba.

"Teema ma za tayi farin cikin ganinki.

Barrister A tayi murmushi ta sace kallon Aliyu, karaf.....suka had'a idanu ya kashe mata idonshi d'aya batasan lokaci da ta lumshe golden eyes d'inta, daga bisani ta bud'e su fesss......akanshi tayi mishi k'ayatattce murmushi, sannan ta bi bayan Zee-zee har suka shige d'akin idanuwan Aliyu suna kanta.

"A lokaci da za'a auna Bp momma za'a iske ya haura d'ari biyu da tamani, tsabar kad'uwa gani abinda Aliyu yake yi wa barrister babban tashin hankalinta bai wuce mayatattace kallon da ya bi ta da shi ba.

"Da kyar ta tattaro 'yar raguwar natsuwarta ta had'a da k'arfin hali ta dube Aliyu da idanuwanta ba bu komai ciki face tashin hankali.

"Sul....tan....!
Ta kira sunanshi cikin rawar murya.

Na'am!"

Ya amsa yana kallonta.

Da fatar kana zaune lafiya da iyalinka?"

"Lafiya qalau momma ba wani matsala.

Shiru ya biyo baya jikin momma ya yi sanyi tana so ta tambayeshi yana had'a shinfid'a da barrister, tana jin tsoron amsar da zai bata.

"Sai kawai tayi ta maza ta gyara zamanta, tana mushirikin murmushi ta ce ina fatar kana sauke hakkinta yadda ya kamata?"

Kallon mamaki yake mata sai kuma ya murmusa tsaff....ya gane idan ta dosa sai ya ce sosai ma kuwa momma duk abinda takeso ina mata.

"Gaban momma ya cigaba da dukan tara-tara babban tashin hankalinta bai wuce asiri da Jarumi ya bata na kashewa Aliyu mazak'uta, sai gashi Aliyu yana fad'a mata yana shagalinshi

to.....ina zance asiri da suka yi mishi ana nufi ya karye.
"Gani yadda ta k'ura mishi idanu ba ko kaftawa yasa ya ce lafiya momma naga kin tsareni da ido, kuma kinyi shiru?"

"Ta shiga kame-kame daga bisani ta yi nasarar cewa anyya kuwa Gadanga kana had'a shinfid'a da yarinyar nan?"
Sam banga jikinta ya nuna hakan ba.
Tafad'a tana tsare shi da idanu, sosai wannan tambayarta ta tabashi haushi da takaici ya 6ata fuska ya ce ki tambayeta momma za ta fad'a miki ko yau kafin mu baro Yola muna tare a d'aki d'aya.
"Please....momma ki daina irin wannan bincike bashida amfani, ni fa ba k'aramin yaro bane duk wani hakke aure nasani.
Kuma ina k'ok'arin sauke shi.
"Ni zan fita sai na dawo."
Ya k'arasa magana had'e da mik'ewa.
A dawo lafiya!
Cewar momma cikin yana yi na tsoro.
"Kaitsaye d'akinsu Zee-ze ya wuce ya tararda su suna fira yayin da Teema na kwance a jikin barrister, sai wasa take da dogon bak'in gashinta.
"Sosai hakan ya yi mishi dad'i saboda yana k'aunar siblings d'inshi ba kad'an ba miskilancinshi ke hanashi nuna musu hakan.
"Tsaye ya yi a bakin k'ofa yana kallonsu da girar ido d'age, Teema na arba da shi ta sha jinin jikinta saboda Allah ya zuba mata tsoronshi.
"Zan fita"
Yafad'a k'asan mak'oshi.

Atsanake tad'ago tana fad'i adawo lafiya Allah ya bada sa'a!

Amin nagode!
Har juya ya sake waigowa ya ce Zainab ba abinci agidan naku ne da ba ki kawo mata ba?"
Ko tsabar rashin iya tar6o guest ne?"
"Cike da tsoro Zee-zee ta ce Yaya kasan momma bata bari adafa abinci da yawa.
Mtsss.....ya ja tsaki had'e da barin d'akin yana cewa ki tabbata kin gayawa chef Emmanuel ya girka mata abinda za ta ci.

Jeeddah Aliyu
[7/27, 12:02 AM] Jiddah Aliyu: *DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA NA KUD'I NE IDAB KANA SO SAI KA TUNTUBE WANNAN NUMBER*
0813943903

*SAI KA TURA SHEDAR BIYANKA GA WANNAN NUMBER*
08166177830
*ZA KA IYA TURAWA WANNAN NUMBER KATIN MTN*
08039424298
*SHEDAR BIYANKA KATINKA GA WANNAN NUMBER*
07084161619

DA D'UMID'UMINSU DAGA ALK'ALUMA SHIDDA

*JIDDAH ALIYU*:-```GIDAN RINA```

*A'ISHA DANSABO*:-```BURIN ZUCIYA```

*KHADIJA AHMAD KDEEY*:-```DA CIWO A ZUCIYATA``

*RAHMA MUH'D RUFA'I NALELLE*:- HAYATUDEEN

*SLIMZY*:- IZZATA

*SAFIYA GALADANCHI*:- TANA K'ASA TANA DABO

*GIDAN RINA*

Not edited!

*23*

Yana k'arasa fita zee-zee ta kalleta tana dariya ta ce gaskiya matar Yaya Yayanmu yana ji da ke, Allah yasa kema haka ki ke ji da shi.
'Yar siriryar dariya tayi ta ce sosai ma kuwa.
Momma wacce tun fitar Aliyu take la6e tana sauraren firar tasu, ta zaro manyan idanuta tana huci, bankad'o k'ofar tayi ba ko sallama ta bi su da kallo.
Gani yadda suma suke kallonta yasa ta wayace ta ce Emmanuel girkin Alhaji zai doura yanzu, Zee-zee ta bi ki ku je flat dinku ta tayaki ki girkawa mijinki abinda zai ci.
"Da sauri Zee-zee ta d'ago tana kallon momma cike da zallan mamaki, ta ce "momma yaushe na iya girki da har zan tayata?"
ki bar Emma ya dafa mata koda noodles ne.
makirin murmushi momma tayi kafin ta ce "miye amfaninta idan bata girkawa mijinta abinci ba?"
Idan ke ba ki iya ba ai ita ta iya
daga yau ki fara girkawa mijinki abinci kinji my daughter?"

Ajiyar zuciya barrister A tayi tana mai cigaba da kallon momma tana karanta yana yinta.
"Har zee-zee za ta sake yin magana barrister A ta katseta da sauri ta hanyar cewa, to momma!
"Momma tayi murmushin mugunta saboda ganinta barrister A ta taso gidan huta uwa-uba yana yin aikinta yaushe take da lokaci shiga kitchen har ta iya wani abu wai shi girki. Atunaninta tun daga wurin girki za su fara samun matsala da Aliyu saboda ta san halinshi da tsirfa, ba ko ne irin abinci yake ci ba.
Saboda haka shiyasa tayi amfani da wannan damar tafara aiwatar da nufinta akansu.
"Shikenan my daughter tashi maza ku tafi ki had'awa yarona delicious, yana ci kunnenshi na motsi.
Ta k'arasa magana tana washe hak'ora na kissa da kissisina.
Hannun Zee-zee barrister A ta rik'o zo mu je Zee ki tayani kema daga yau ki fara learning.
"Ni ma zan je matar Yayanmu!
Cewar Teema tana sosa gashin kanta.
Kafin barrister A tayi magana har momma ta rigata cewa kema bi su ki koya.
"Har suka fice daga d'akin momma tana murmushinta na zallan mugunta.
Da suke iso compound idanuwan barrister A suka hango apartment d'in Maryam, ta k'urawa wurin idanu tana mamaki yadda aka bar barandar wurin tayi k'ura, musanmman da tayi la'akari ko ina na gidan tsaf-tsaf yake idan ka cire wurin.
Ajiyar zuciya ta yi ta kauda ganinta suka k'arasa flat d'inta.
A falon k'asa suka zauna zee-zee ta had'a kayan kallo, suna cikin kallo aka yi kiran sallar la'asar, har barrister A tayi sallah ta dawo bata ga alamar Zee-zee da Teema zasu tashi suyi sallah ba.
Sai tunanin dukansu suna period ne, don haka ta share su suka cigaba da kallonsu.
"K'arfe 5:00 ta buga Zee-zee ta kalli barrister A ta ce matar Yaya kin ce sai kin yi sallah, za mu doura girki gashi har 5:00 o'clock ya yi.
"Barrister A tayi murmushi tana fad'i ko za mu fara girki nan zee-zee saidai gobe, saboda na duba a store ba foodstuffs, kinga zuwa gobe Yayanki zai siyo.
